
# Gujewa daga Ilhadi (Musanta samuwar Allah) zuwa Musulunci

شركاء التنفيذ:

دار الإسلام جمعية الربوة رواد الترجمة المحتوى الإسلامي

يتاح طباعة هذا الإصدار ونشره بأي وسيلة مع الالتزام بالإشارة إلى المصدر وعدم التغيير في النص.

Telephone: +966114454900
ceo@rabwah.sa
P.O.BOX: 29465
RIYADH: 11557
www.islamhouse.com


بسم الله الرحمن الرحيم

## Tambaya da amsa

Da sunan Allah, godiya ta tabbata ga Allah, kuma tsira da amincin Allah su tabbata ga Manzon Allah, da Alayan sa da Sahabban sa da kuma waɗanda suka jiɓince shi؛ bayan haka:

Wannan wani ɗan ƙaramin littafi ne: "Gujewa daga ilhadi (Musanta samuwar Allah) zuwa musulunci".

Dan ƙaramin littafin zai gabatar da wani bayani ga "Dabi'ar ilhadi' da matsalolin sa, kuma yaya Ilhadi yake warwara idan ya haɗu da abubuwa bayyanannu na hankali da ɗabi'ar da aka halicci mutum da ita.

Kuma ɗan littafin zai bujiro da sashin dalilain tabbatar da samuwar mahallici - tsarki ya tabbatar maSa -.

Mu muna sanin Allah - mai girma da ɗaukaka - da hankali, Allah - maɗaukakin sarki - Ya ce:

﴿أَمۡ خُلِقُواْ مِنۡ غَيۡرِ شَيۡءٍ أَمۡ هُمُ ٱلۡخَٰلِقُونَ ٣٥﴾ [الطور: 35]

{Shin, an halitta su ne bã daga kõme ba, kõ kuwa sũ ne mãsu yin halitta ?} [Surat : Al-Dur : 35].

A hankalce, anan akwai abubuwa uku da zasu iya yuyiwa, basu da na huɗu :

Na farko: yakasance an haliccemu ba tare da mahallici ba (Shin, an hallice su ne ba tare da komai ba) wannan korarre ne, dan ta yaya za'a halicce mu ba tare da mahallici ba?

Na biyu: Ya zama mun halicci kawunan mu (Ko kuma sune masu yin halittar), wannan korarrene, kuma, dan ta yaya zan halicci kaina kafin a halicce ni?

A wannan lokacin ta hanyar hankali abinda zai iya yuyiwa na uku zai rage, shine wanda ayar mai girma tayi shiru game dashi؛, domin cewa shi shine abu mabayyani, cewa lallai muna da wani mahallicin da ya halicce mu.

To mu muna sanin Allah ta hanyar hankali.

Hakanan mu muna sanin Allah, da ɗabi'ar da aka halicce mu akan ta.

Kuma muna sani da ɗabi'ar mu wacce aka halicce mu akanta, cewa gumaka da ɗabi'a basa mallakar iko abisa halittar kasantacce, ko abisa samar da ƙwayoyin cuta da mutum, ko abisa kiyaye ayyukan jikin mutum, ta hanyar wannan surar, ko abisa kyautata halitta daga ƙwaya zuwa Majarrah (Gurine a sama acikin sa akwai tarin taurari).

Gumaka waɗanda kafirai suke bauta musu, da ɗabi'ar da masu musanta samuwar Allah suke yin imani da ita kowannan su mai buƙatuwa ne ga mahaliccin sa.

Gumaka ko ɗabi'a basa mallakar wani abu daga al'amarin su, kuma basu da wani iko akan kiyaye sanadari ajikin halittu da yake sanya tasiri ga ƙwayoyin halitta acikin ka ta hanyar wannan gwargwadan mai ɗimautarwa, kuma basu da iko akan sanya kaifin gado, waɗanda sune miliyoyin ababen sani a cikin kowace madda (Itace wadda kowane mai rai yake kasancewa da ita), kuma basu da iko abisa samar da kowane abu kai harma abisa samar da kan su.

To mahaliccin wannan duniyar da waɗannan abubuwan mamakin. shine Mahalicci, Mai girma, Masani, mai iko, Gwani - tsarki ya tabbatar masa -.

Sannan bayan haka, ɗan karamin littafin zai tattauna abubuwa masu rikitarwa na masu kore samuwar Allah, da ƙoƙarin su na ɓata hujjojin samuwar mahalicci na hankali, da ɗabi'ar da aka halicci mutum akan ta.

Daga mafi sharar ɓatawar su faɗar "Bijirowar bayyanar kasantacce katsahan", sun faɗi hakanne saboda rashin fahimtar su, ko dan jahiltar su ga tushen abubuwan daza su iya faruwa؛ domin bijrowa katsahan, tana da sharuɗɗa biyu basa rabuwa daga gare ta.

Sune: Zamani da guri.

Bijirowa katsahan tana sharɗanta wani zamanin da zata tabbata acikin sa da farar da gurbin ta.

Kuma tana sharɗanta samuwa ta madda ta wuri da zata tabbata acikin sa, ta hanyar fitar da abin aikatawar ta.

To, ta yaya zamuce da wani ƙoƙari ga bjiirowa katsahan acikin samar da kasantacce, tare da cewa kasancewar mu yazo daga rashin zamani da rashin guri, daga nan kuma daga rashin bijrowa katsahan !

Sannan ɗan littafin zai bijiro ga wasu dalilai na hankali, akan larurar samuwar Addini, da ma'anar Addinin da larurar miƙa wuya ga Ubangijin talikai da jawuwa gareshi - tsarki ya tabbatar maSa -, miƙa wuya ga Allah, da jawuwa gareshi shine : Haƙiƙanin Addini.

Kai kana ƙanƙar da kai ga Allah, kuma kana bauta ga Mahaliccin ka Mai azirta ka,kuma Mai baiwa gare ka da dukkanin baiwa da ni'ima da shiriya.

Ibada itace haƙƙin Allah akan bayin Sa, domin cewa shi - tsarki ya tabbatar maSa - shine wanda Ya haliccemu ya raya mu, Ya azirta mu Ya shiryar damu, ya aiko mana da Manzannin Sa dan ya jarraba mu, waye acikinmu mafi kyautata aiki, to Ibada itace haƙƙin Allah akan mu.

﴿ٱلَّذِى خَلَقَ ٱلْمَوْتَ وَٱلْحَيَوٰةَ لِيَبْلُوَكُمْ أَيُّكُمْ أَحْسَنُ عَمَلًا ۚ وَهُوَ ٱلْعَزِيزُ ٱلْغَفُورُ ۝٢﴾ [الملك: 2]

{Shi ne Wanda Ya halitta mutuwa da rãyuwa domin Ya jarraba ku, Ya nũna wãye daga cikinku ya fi kyãwon aiki, Shi ne Mabuwãyi, Mai gafara}.{2}. [Surat AlMulk : 2].

Sannan a mataki mai bi, ɗan ƙaramin littafin zai gabatar da wasu dalilai akan ingancin Musulunci, da bayanin haƙiƙanin cewa, Allah baya karɓar wani Addini daga mutum inba Musulunci ba, Allah - maɗaukakin sarki - Ya ce :

﴿وَمَن يَبۡتَغِ غَيۡرَ ٱلۡإِسۡلَٰمِ دِينٗا فَلَن يُقۡبَلَ مِنۡهُ وَهُوَ فِي ٱلۡأٓخِرَةِ مِنَ ٱلۡخَٰسِرِينَ٨٥﴾ [آل عمران: 85]

{Kuma wanda ya nẽmi wanin Musulunci ya zama addini, to, bã zã a karɓa daga gare shi ba. Kuma shi a Lãhira yana daga cikin mãsu hasãra} {85}. [Surat Aal-Imran: 85].

Musulunci shine Addinin wanda Allah Ya aiko dukkanin Annabawa da Manzanni da shi.

Alamar Musulinci ta asali, lallai cewa: Acikinsa akwai ma'anar miƙa wuya ga Allah da bautawa Allah Shi kaɗai.

Musulunci shine mafi cikar Shari'a da take kwaɗaitarwa akan miƙa wuya ga Allah.

Kuma shine Addini ɗaya, wanda yake kira ga kaɗaita Allah, wannan Tauhidin wanda dukkanin Annabawa suka zo da shi.

Dukkanin Annbawa suna kan Aƙidar Tauhidi, koda Shari'un su sun banbanta.

Allah - maɗaukakin sarki - ya ce :

﴿وَمَآ أَرۡسَلۡنَا مِن قَبۡلِكَ مِن رَّسُولٍ إِلَّا نُوحِيٓ إِلَيۡهِ أَنَّهُۥ لَآ إِلَٰهَ إِلَّآ أَنَا۠ فَٱعۡبُدُونِ٢٥﴾ [الأنبياء: 25]

{Kuma ba Mu aiki wani Manzo ba a gabãninka fãce Munã yin wahayi zuwa gare shi, cẽwa "Lalle ne Shi, bãbu abin bautãwa fãce Nĩ, sai ku bauta Mini} {25}. [Surat Al-Anbiya: 25].

Babu wani Addinin da ya rage a yau a bayan ƙasa, da yake akan wannan Tauhidin, inba Musulunci ba, yayin da dukkanin masu dangantuwa ga wasu Shari'un daban, wani rabo na shirka ya wayi gari agaresu, ya ƙaranta ko ya yawaita, bayan mutuwar Annabawa, kuma bayan sun bar mutane akan Tauhidi, sai mutane suka riƙi shirkoki tare da shudewar lokaci, babu wani Addinin da ya rage a yau da yake akan tsarkakakken Tauhidin da Annabawa suka zo dash,i inba Musulunci ba.

Sannan ɗan ƙaramin littafin zai rufe da bayanin ta yaya mutum zai wayi gari yana musulmi, da ma'anar Musulunci da larurar Musulunci.

Mususlunci ya amsa dukkanin samammun tambayoyi waɗanda suke kai kawo acikin tinanin kowane mutum: Daga ina mukazo, kuma me yasa muke a nan acikin wannan duniyar, kuma zuwa ina zamu tafi?

Musulunci ya amsa dukkanin wannan acikin Aya ɗaya daga Al-kur'ani mai girma, Ubangijin mu - tsarki ya tabbatar maSa Ya ce:

﴿وَمَالِيَ لَآ أَعۡبُدُ ٱلَّذِي فَطَرَنِي وَإِلَيۡهِ تُرۡجَعُونَ٢٢﴾ [يس: 22]

{Kuma mene ne a gare ni, bã zan bauta wa Wanda Ya ƙãga halittata ba, kuma zuwa gare Shi ake mayar da ku?}. [Surat yasin: 22].

Daga ina kazo? Allah shine wanda Ya haliceni (Ya ƙagoni).

Kuma ina ni zan tafi ? Da sannu zan tafi zuwa ga Allah, dan ayi mini hisabi akan aikina. (Kuma gare Shi za'a komar daku).

Saboda me yasa nazo wannan duniyar ? Dan bautar Allah, dan kuma a jarrabani.

Dan me yasa nake bautawa Allah ? Yana daga ɗabi'a in bautawa Allah wanda Ya ƙageni, to wannan itace ɗabi'ar alaƙa tsakanin bawa da Ubangijin sa cewa : Bawa ya bautawa Ubangijin sa kuma Mahaliccin sa. ("Kuma mene ne a gare ni, bã zan bauta wa Wanda Ya ƙãga halittata ba, kuma zuwa gare Shi ake mayar da ku ?". Aya ɗaya ta tattaro amsar mafi muhimmancin tambayoyi ukun, waɗanda mutum yake ɗimaucewa dasu.

﴿وَمَالِىَ لَآ أَعۡبُدُ ٱلَّذِى فَطَرَنِى وَإِلَيۡهِ تُرۡجَعُونَ﴿٢٢﴾﴾ [يس: 22]

{Kuma mene ne a gare ni, bã zan bauta wa Wanda Ya ƙãga halittata ba, kuma zuwa gare Shi ake mayar da ku?}. [Surat yasin: 22].

Musulunci shine Shari; ar Allah ga talikai.

Musulunci yana nufin, bawa ya miƙa kansa ga Allah, sai ya ƙanƙar da kai ga Allah, ya kuma jawu gareshi da biyayya, ya miƙa wuya ga Mahaliccin sa kuma majiɓincin al'amuran sa.

Allah - maɗaukakin sarki - Ya ce

﴿وَمَن يُسۡلِمۡ وَجۡهَهُۥٓ إِلَى ٱللَّهِ وَهُوَ مُحۡسِنٞ فَقَدِ ٱسۡتَمۡسَكَ بِٱلۡعُرۡوَةِ ٱلۡوُثۡقَىٰۗ وَإِلَى ٱللَّهِ عَٰقِبَةُ ٱلۡأُمُورِ ٢٢﴾ [لقمان: 22]

{Kuma wanda ya mĩka fuskarsa zuwa ga Allah, alhãli kuma yanã mai kyautatãwa, to, lalle ya yi riƙo ga igiya amintacciya} {22}. [Surat Luƙman : 22].

Musulunci yana nufin tabbatar da bauta ga Allah, a cikin kowane abu ƙarami da babba, acikin rayuwar ka, Allah - maɗaukakin sarki - Ya ce :

﴿قُلۡ إِنَّ صَلَاتِي وَنُسُكِي وَمَحۡيَايَ وَمَمَاتِي لِلَّهِ رَبِّ ٱلۡعَٰلَمِينَ ١٦٢ لَا شَرِيكَ لَهُۥۖ وَبِذَٰلِكَ أُمِرۡتُ وَأَنَا۠ أَوَّلُ ٱلۡمُسۡلِمِينَ ١٦٣﴾ [الأنعام: 162-163]

{Ka ce: "Lalle ne sallãta, da baikõna, da rãyuwãta, da mutuwãta, na Allah ne Ubangijin tãlikai} {162}. {Bãbu abõkin tãrayya a gare Shi. Kuma da wancan aka umurce ni, kuma ni ne farkon mãsu sallamãwa} {163}. [Surat Al-An'am: 162-163].

Sallata, da ibada ta, da rayuwa ta, da mutuwa ta, na Allah ne Ubangijin talikai: Kowane abu da nake aikata shi na Allah ne, ni ina yin sallah saboda Allah, ina bin mahaifa na sabo da Allah, ina muzakara ina neman ilimi don in amfanar da mutane sabo da Allah, ina yin bacci don in zama mafi ƙarfi a gobe, akan aikata abin da Allah Ya umarce ni da shi.

Ita bauta ce ga Allah, a kowane aiki, waɗannan suna daga mafi muhimmancin mabayyanai da alamomin miƙa wuya ga Allah.

Yunwa abar sani...yunwa dan sanin mafi muhimmancin abin da zai shagaltar da mu, ba mai ƙosar da ita sai Mususlunci...

Yayin da Ilhadi baya isar mutum yasan cewa shi an haifeshine dan ya mutu.

Dan ƙaramin littafin yana misalta: Wani wajabci gwargwado na ilimi da hankali, acikin rikice-rikicen musanta Allah, da sashin dalilan ingancin Musulunci.

Wajabcin (zai zamo) da sigar tambaya da amsa...

To kazo mu fara da albarkar Allah

1- Menene ma'anar Ilhadi?

Amsa: Ilhadi shine bijirewa ƙudirewa da dukkanin wani ƙarfi na ɓoye.

Mulhidi yana musun Mahalicci da Annabci, da tashin Al-ƙiyama.

2 - Me kuke aibatashi dangane Ilhadi ?

Amsa : Ilhadi yana neman wani imani mafi ɗaukaka da yawa, daga imani na Addini.

Saidai cewa shi imanine abin ginawa akan ƙaddare-ƙaddare, masu ɗimautarwa, da raye-raye na kuskure, saɓanin imani na Addini abin ginawa akan bayyanannun abubuwa na ɗabi'ar da aka halicci mutum akansu, da abubuwa a yanke da muke lura da su da idanuwan mu da na farko-farkon hankali da hujjojio na Shari'a.

Har kada ayi maka Ilhad, to ka raya abin da zaizo ɗin nan : A- Abin da babu ne aka raɓa shi da abin da babu sai ya zama wani abu mai girma...ya zama kasantacce mai ɗimatarwa daga mafi ƙayatarwar abinda yake kasancewa da kuma ƙarshen ma,aune masu zirfi, da iyakoki maƙuntata. B- Bijirowar katsahan ta fitar da iyakoki masu ƙunci, da tabbatattun fiziyya (kimiyar ɗabi,a) waɗanda duniya tazo da su, a yayin da cewa

sharuɗɗa biyu na bijirowar katsahan, sune guri da zamani, kuma kasantacce yazo ne daga rashin guri da zamani daga nan kuma daga rashin bijirowar katsahan C- Rashin tsari da yanayi na ƙasa na farko sun haifar da rayuwa, kuma sun farar da ƙwayar cuta, da kuma mutum, a yayin da cewa hankalin mutum yana ƙololuwar kaifin sa a yanzu, bashi da ikon ya samar da mafi ƙarancin surorin rayuwa. D- Dukkanin darajoji na ɗabi'a, waɗanda muke miƙa wuya ga ingancin su, waɗanda mafi yawansu suke tafiya a cikin fuskanta ta kishiyanta ga madda a cike - ɗabi'u na asali suna misalta wani nauyi na dukiya da tabewa, abisa matakin maslahar duniya - su suna daga ababen badawa na madda da ababen samarwar su, Waɗan nan ƙoƙari na hankali ya wajaba akanka kayi imani da su har ka fara Ilhadi.

E- Ba'a samun wata madogara ta hankali ko ta madda acikin Ilhadi, dazata hana ƙarar da mutanen ƙasa gaba ɗaya.

Shin duniyar madda batasan kuskure bane ko daidai?

A wannan lokacin, sai ƙarar da mutanen ƙasa gaba ɗaya da rayasu sukayi daidai a Ilhadi.

Ilhadi shima maginar sa akan imani ne, sai dai imani ne, ba tare da samo gurbin sa daga wani ilimi ko ciratowa (riwayar sa) ko hankali ko ɗabi'u ba.

3- Menene dalili akan samuwar Mahalicci?

Amsa: Dalilan suna da yawa sai dai zamu isu da dalilai biyu:

1- Dalilin samarwa.

2- Dalilin kulawa da kyautatawa.

3- Menene ma;anar dalilin samarwa?

Amsa: Dalilin samarwa yana nufin cewa:

Kowane abu fararrene wato an samar dashi bayan bai kasance samamme ba, ba makawa yana da mai fararwa wato:Mai samarwa.

Saboda haka a tare da mu, akwai abin da baya taƙaituwa gareshi na dalilai akan samuwar Mahalicci - tsarki ya tabbatar maSa -.

Kowacce ƙwaya a duniya, ita dalilice akan halitta, dan kowane abu fararre, haƙiƙa ya bayyana zuwa samuwa, to shi: Dalili ne ga Mahalicci Mai samarwa.

Kai idan ka duba zuwa samammu, zai bayyana gareka cewa, shi mai bijirowane kuma mai canjawane ba madawwami bane ko na azali, idan haka ne, to shi ba mai isuwa bane da zatinsa, wannan zai sanyaka ka yanke da hankalin ka da cewa yana da wani Mahalicci, bayan nan ganinka zai juya zuwa Mai samarwa da zarar duba ga talikai.

Saboda haka ya mamakin yawan Ayoyin Al-ƙur'ani acikin juya duba zuwa talikai da samammu a gefan mu, Allah - maɗaukakin sarki - Ya ce:

﴿قُلِ ٱنظُرُواْ مَاذَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۚ وَمَا تُغۡنِي ٱلۡأٓيَٰتُ وَٱلنُّذُرُ عَن قَوۡمٖ لَّا يُؤۡمِنُونَ ١٠١﴾
[يونس: 101]

{Ka ce : "Ku dũbi abin da yake cikin sammai da ƙasa."Kuma ãyõyi da gargaɗi bã su wadãtarwa ga mutãne waɗanda bã su yin ĩmãni.{101}. [Surat Yunus : 101].

Kuma Allah - maɗaukakin sarki - Ya ce :

﴿أَوَلَمۡ يَتَفَكَّرُواْ فِيٓ أَنفُسِهِمۗ مَّا خَلَقَ ٱللَّهُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضَ وَمَا بَيۡنَهُمَآ إِلَّا بِٱلۡحَقِّ وَأَجَلٖ
مُّسَمّٗىۗ وَإِنَّ كَثِيرٗا مِّنَ ٱلنَّاسِ بِلِقَآيِٕ رَبِّهِمۡ لَكَٰفِرُونَ ٨﴾ [الروم: 8]

{Ah Shin, ba su yi tunãni ba a cikin zukãtansu cẽwa Allah bai halitta sammai da ƙasa ba da abin da ke tsakãninsu, fãce da gaskiya da ajali ambatacce ? Kuma lalle mãsu yawa daga mutãne kãfirai ne ga gamuwa da Ubangijinsu ?} {8} [Surat Al-Rum : 8].

kuma Allah - maɗaukakin sarki - Ya ce:

﴿أَوَلَمۡ يَنظُرُواْ فِي مَلَكُوتِ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِ وَمَا خَلَقَ ٱللَّهُ مِن شَيۡءٖ وَأَنۡ عَسَىٰٓ أَن يَكُونَ قَدِ ٱقۡتَرَبَ أَجَلُهُمۡۖ فَبِأَيِّ حَدِيثِۭ بَعۡدَهُۥ يُؤۡمِنُونَ١٨٥﴾ [الأعراف: 185]

{Shin, basuyi dubi ba a cikin mulkin sammai da kasa, da kuma abinda Allah ya halitta daga komai} {185}. [Surat Al-A'araf: 185].

Dukkanin wani abu abin fararwa, to shi: Dalili ne kai tsaye ga Mai samarwa!

5- Menene ma'anar dalilin kulawa da kyautatawa?

Amsa: Dalilin Kulawa da kyautatawa yana nufin cewa:

Kowane abu a samuwa, a sake ba ƙaidi, daga ƙwayoyin komayya - mafi ƙanƙantar jiki na madda da kafashi ya cika, yana kama da ƙwayar kofy - yana ɗaukar matakin daga matakan ƙullewa ta aiki. .

Wato yana bada wani aiki abin keɓantawa da wata muhimma abar iyakancewa.

Dukkanin ƙulli na aiki acikin ɗabi'a, shi daraja ne mai ƙaruwa, akan tsantsar samuwa.

Samuwa matsayi ce.

Kulli kuma mai shiga samamman abu, shi matsayi ne mai ƙaruwa akan tsantsar samuwa.

Dukkanin abinda ke gefan ka, abin ƙerawa ne da kamanni abin ayyanawa, dan ya bada aikin sa abin iyakancewa.

A wannan yayin dukkanin abinda ke gefan ka yana ɗaukar wani ƙulli na aiki.

Kulli na aiki shi dalili ne, na aikatawa da samarwa.

A wannan yayin, ba makawa daga Mai samarwa.

Misalin wannan "Fitila": Wannan yana misalta ƙulli na aiki.

Fitilar wutar lantarki tana haɗuwa daga:

1- Kwan fitila.

2- Waya ta darma; Zata sadar da wutar lantarki ga ƙwan fitilar.

3- Gas ɓoyayye Yake kare ƙwan fitilar amma baya aiki tare da ita ko tare da wutar lantarkin.

4- Gilas: Yana hana shigar iska ko fitar gas ɗin ɓoyayye, in ba haka bafa da fitilar ta ƙone.

5- Ka'idar fitilar: Ana sadar da fitilar, da rufi kuma ta kasance matafiya ga ciratar wutar lantarki.

Anan fitilar wutar lantarki, wani tsari ne acikinsa akwai ƙulli bazai yiwu a shinfiɗa bayanin sa ba, bayan nan acikin sa akwai nuni na hankali na farko da yake fa'idantar da aiki abin kyautatawa.

Mutumin da yake kore aiki abin kyautatawa game da fitila, ko yake ƙaddara bayyanars a ta katsahan, shine abin nema da dalili akan hakan!

Wanda ya ƙera fitilar,yana sani ƙwarai ma'anar wutar lantarki da matafiyun ta da amfanin fitilar da tasirantuwar fitilar,sabo da haka samuwar fitila dalili ne kai tsaye, akan cewa tana da wanda yayi ta mai kyautatawa, ba wani nau'i ne mara tsari ba cewa kawai anan akwai fitilu mabanbanta a kamannin su, cikakku daga gare shi!

A irin wannan mataki, na kafa hujja na hankali zamu samu cewa ƙullallan abu a aikace, misalin mutum ne, yana da mai samarwa mai yinsa.

Fitila tana kasancewane daga ababe biyar:

Yayin da mutum yana kasancewa ne,daga abin kasancewa biliyan huɗu a cikin kowacce ƙwayar garkuwa daga ƙwayoyin garkuwa na halittar sa.

Abin tabbatarwa guda biliyan huɗu "Harafi ne" da suke kamanta ayyukan kasantacce rayayye, itace ake ambatan ta: Kwayar halitta ta gado, ko DNA waɗan nan haruffan suna samuwa acikin kwalfar gurtsun kowace ƙwayar garkuwa daga garkuwannin halittar ka.

Idan kayi zatan cewa abubuwa biyar da suka haɗa futila kuma suka keɓantu da ita, suna da wanda yayi su, kai kuma baka da wanda yayi ka, to wannan matsalar ka ce kai kaɗai.

﴿أَمۡ خُلِقُواْ مِنۡ غَيۡرِ شَيۡءٍ أَمۡ هُمُ ٱلۡخَٰلِقُونَ ٣٥﴾ [الطور: 35]

{Shin, an halitta su ne bã daga kõme ba, kõ kuwa sũ ne mãsu yin halitta ?} (35). [Surat : Al-Dur : 35].

Dukkanin wani abinda ke gefan ka, acikin sa akwai ƙulli, ba'a samun wani abu acikin ɗabi'a ko acikin ƙwayar komayya, ko acikin falakai ko acikin jikin ka a sake, ba tare da wani gwargwado na ƙullin aiki ba.

Kulli na aiki da aiki ga kowace ƙwayar komayya, da kuma dukkan na jiki, su wasu al'amura ne samammu acikin kowane abu acikin kasantattu.

Allah - maɗaukakin sarki - Ya ce :

Y las aleyas coránicas son abundantes sobre este tema :

﴿ٱلَّذِينَ ءَاتَيۡنَٰهُمُ ٱلۡكِتَٰبَ يَعۡرِفُونَهُۥ كَمَا يَعۡرِفُونَ أَبۡنَآءَهُمۡۖ وَإِنَّ فَرِيقٗا مِّنۡهُمۡ لَيَكۡتُمُونَ ٱلۡحَقَّ وَهُمۡ يَعۡلَمُونَ ١٤٦﴾ [البقرة: 146]

{Lalle ne, a cikin halittar sammai da ƙasa, da sãɓãwar dare da yini, da jirãge wadaɗnda suke gudana a cikin tẽku (ɗauke) da abin da yake amfãnin mutãne, da abin da Allah Ya saukar daga sama daga ruwa, sai Ya rãyar da ƙasa da shi a bãyan mutuwarta, kuma Ya wãtsa, a cikinta, daga dukan dabba, kuma da jũyãwar iskõki da girgije hõrarre a tsakãnin sama da ƙasa; haƙĩƙa, akwaiãyõyi ga mutãne mãsu yin hankali} {14}. [Surat Al-bakara: 164].

Ayoyi a akan wannan suna da yawa sosai.

Ba mai tinawa sai wanda yake amfani da hankalin sa.

﴿هُوَ ٱلَّذِيٓ أَنزَلَ عَلَيۡكَ ٱلۡكِتَٰبَ مِنۡهُ ءَايَٰتٞ مُّحۡكَمَٰتٌ هُنَّ أُمُّ ٱلۡكِتَٰبِ وَأُخَرُ مُتَشَٰبِهَٰتٞۖ فَأَمَّا ٱلَّذِينَ فِي قُلُوبِهِمۡ زَيۡغٞ فَيَتَّبِعُونَ مَا تَشَٰبَهَ مِنۡهُ ٱبۡتِغَآءَ ٱلۡفِتۡنَةِ وَٱبۡتِغَآءَ تَأۡوِيلِهِۦۖ وَمَا يَعۡلَمُ تَأۡوِيلَهُۥٓ إِلَّا ٱللَّهُۗ وَٱلرَّٰسِخُونَ فِي ٱلۡعِلۡمِ يَقُولُونَ ءَامَنَّا بِهِۦ كُلّٞ مِّنۡ عِندِ رَبِّنَاۗ وَمَا يَذَّكَّرُ إِلَّآ أُوْلُواْ ٱلۡأَلۡبَٰبِ ٧﴾ [آل عمران: 7]

{Ba mai tinawa sai ma'abota hankali} {7}. [Surat Aal-Imran : 7].

Duk wanda yayi amfani da hankalin sa, ya kuma yi duba acikin samuwa (dalilin samarwa) yayi duba acikin kiyayewa da ayyukan samammu (Dalilin kulawa da kyautatawa) zai yanke kai tsaye da ingancin shiryarwar mai samarwa a hankalce !

6- Me yasa mutum da waninsa daga kasantattu rayayyu basa kasancewa mafararsu kasantattu na farko ƙananu sosai ?

Amsa : Anan akwai matsaloli biyu :

Matsala ta farko : Lallai cewa shi ba'a samun wani dalili guda ɗaya abin lura abisa ciratar wani nau'i daga kasantattu rayayyu zuwa wani nau'in daban, ballantana daga wannan zabura ta ƙaddarawa mai tsoratarwa, da cewa mutum yazo daga kasantattu na fari.

To ta yaya mai musanta samuwar Allah, zaiyi imani da wannan ƙaddarawar abar rasawa, daga kowane dalili na kai tsaye, kuma yana yi mana musun kafa hujja ta hankali ta Addini ?

Matsala ta biyu : Dacewa da nazariyya ta mafi ƙarancin ƙwayar gado baya yiwuwa ga kasantacce rayayye, duk yanda ƙanƙantarsa take, da ya sauka zuwa mafi ƙaranci daga ƙwayar gado 200.

Kuma mafi ƙarancin iyaka, daga ƙwayoyin gado shine : Gwargwado mafi ƙasaƙanci daga ƙwayoyin halitta na gado wanda wani kasantacce rayayye baya rayuwa batare da shi ba!

Wani kasantacce rayayye bazai kasance ba da ace adadin ƙwayoyin halittar sa na gado sunyi ƙasa daga iyakar mafi ƙaranci daga gwargwadan ƙwayar gado ɗaya.

Gane (Kwayar halitta ta gado) : Wani zarene na bayanai, mai ƙunshe da wani adadi babba na lambobin ƙwayoyin halitta na gado waɗanda ke tsara bayanai na halittu.

Anan akwai mafi ƙarancin adadin ƙwayoyin halitta na gado da ake buƙata dan rayuwa ta yanda : Waɗan nan ƙwayoyin halittar na gado ke tsara makamashi - saboda halitta mai rai bazai iya rayuwa ba batare da makamashin da zai sashi kuzari ba - wasu taron ƙwayoyin halitta na gadon dake tsarawa dan abinci, da wasu ƙwayoyin gadon daban suna tsarayawa dan yawaita, da wasun su da suke tsarawa dan ainihin ayyuka na rayuwa, haka nan !

Malamai sun tsaya da kirga iyaka mafi ƙaranci daga ƙwayoyin halitta na gado mai lazimtar rayuwa, sun tabbatar da cewa su baya yiwuwa suyi ƙasa da kwayoyin halitta na gado ɗari biyu.

Haƙiƙa cibiyar Craig Venter ta binciko cewa, iyaka mafi ƙaranci daga ƙwayoyin halitta na gado bazai kasance mafi ƙaranci ƙwayoyin halitta na gado ɗari uku da tamanin da biyu ba[1].

Haƙiƙa malamai sun samu cewa, Mycoplasma (Ita wata ƙwayar cuta ce) itace mafi ƙanƙantar kasantacce rayayye samamme a bayan ƙasa a sake ba ƙaidi, tana da ƙwayoyin halitta na gado 468.

---

1 J. Craig Venter Institute (JCVI) sun gudanar da wani bincike dan su gano dukkanin sashin ƙwayoyin halitta masu mahimmanci wanda yake tasiri akan yadda surar jiki da ɗabi'un halitta zai kasance ta hanyar yin gado na M. genitalium ta hanyar ɗaukar ƙwayoyin halittar zuwa wani ɗan ƙanƙanin ƙwaya acikin tantanin halittar wani jikin daban ta yanda zai canja a amfanin su ƙwayoyin halittar. A sakamkon haka sun gano cewa kaso 382 cikin 482 daga cikin ƙwayoyin halitta da suke canja dukkan bayanai acikin ƙwayoyin da suke tasirantar da gado izuwa sanadarin furotin (Protein) duk suna da muhimmanci.

Da al'amarin yakasance madda ne kawai, su kuma halittu tsantsar tsarine na madda, to mu muna cikin buƙatuwa zuwa mu faro daga sifili na ƙwayar halitta ta gado, idan muna nufin wucewa daga sanadarin Haidarojin (Shi wata iskane mara ƙanshi mara kala da yake a lamba ta ɗaya ajerin lambobin sanadarai na abubuwa) zuwa mutum !

Sai dai cewa ilimi yana bamu labari cewa shi, ba'a samun wani abu da ake kira ƙwayar gado ta sifili, ko ƙwayar gado ɗaya, ko kai ƙwayar gado ɗari, ilimi yana cewa : Lallai mu muna cikin buƙatuwa zuwa wasu tattaro masu girma na daga ababan sani, kamar iyaka mafi ƙaranci, in ba haka bafa kasantacce mai rai da bai bayyana ba tun daga farko.

Babu wani abu na farko a cikin ɗabi'a, kai duk wani tsararren abu ya fara ne da wani kiɗimewa mai zaman kansa.

Kuma wannan kiɗimewar zata wanzu a cikin tsarin abin sani, wanda yake tsarawa ga kasantattu kafin su bayyana, wannan kiɗimewar zata wanzu har abada, dutsen tintuɓe a fuskar musanta samuwar Allah, dutsen tntuɓe a fuskar mai msun halittar Allah !

Kai kana gaban keɓantaccen abin sani biliyan huɗu - waɗancan bayanan samammu acikin kwalfar gurtsun kowace ƙwayar garkuwa daga ƙwayoyin garkuwar ka, na asali, domin samar da ayyuka na rayuwa masu muhimmanci.

Mai musanta samuwar Allah. yakasance yana riyawa cewa anan akwai kasantattu, da suka faro daga sifili na ƙwayar gado, sai dai nazariyyar iyaka mafi ƙaranta, daga ƙwayoyin gado lalle zasu ga bayan wannan mafarkin.

Kasantattu rayayyu, sun bayyana ababen kullewa a ayyuka tun daga karon farko, in ba haka bafa da basu bayyana ba tun farko !

7- Menene misalai akan dalilin kulawa da kuma kyautatawa ?

Amsa : Misalan baza su taƙaitu ba.

Kuma littatttafan dake kan ƙasa, baza su yalwace su ba.

﴿وَلَوْ أَنَّمَا فِي ٱلْأَرْضِ مِن شَجَرَةٍ أَقْلَٰمٌ وَٱلْبَحْرُ يَمُدُّهُۥ مِنۢ بَعْدِهِۦ سَبْعَةُ أَبْحُرٍ مَّا نَفِدَتْ كَلِمَٰتُ ٱللَّهِ إِنَّ ٱللَّهَ عَزِيزٌ حَكِيمٌ ۝٢٧﴾ [لقمان: 27]

{Kuma dã dai abin da ke a cikin ƙasa duka, na itãce, ya zama alƙalumma, kuma tẽku tanã yi masa tawada, a bayansa da waɗansu tẽkuna bakwai kalmõmin Allah ba zã su ƙãre ba. Lalle, Allah Mabuwãyi ne, Mai hikima} {27}. [Surat Luƙman :27].

Kowace ƙwayar komayya, a cikin kasnatattu, ita dalilin kulawa ce, mun sani a yau, ko kuwa zamu sani gobe da wannan haƙiƙar.

A- Insulin - sanadarin da yake tasiri a jikin halitta wanda yake narka glucose (sukari), wanda Pancrease yake fitar dashi da ainihin gwargwadan sukarin da ka shashi.

B- Karfin bugawar zuciya ga jini, tana daidai tare da kuzarin da gaɓɓai suke buƙata gwargwadan ƙoƙarin da akayi.

C- Kananun ƙofofin uwar hanjin ka dan kada abincin ya komo zuwa bakin ka sai ka cutu.

D- Kananun ƙofofin fitarwa dan kada tufafin ka su cutu a kowane lokaci.

E- Kasusuwan mahaɗar ƙeyar ka, basa haɗuwa har sai ka sauko daga cikin mahaifiyar ka, kana mai amintacce da sauƙi, domin cewa su da sun kasance a haɗe suke da baka sauko daga cikin mahaifiyar ka ba, sai bayan sun karye, kuma girman su ba zai cika ba. har sai girman ɓargwan ka ya cika.

F- Dukkanin hanyoyin da siginar (Abubuwan da suke motsa jijiyoyi) din jijiyoyin ka da waɗanda suke watsa siginar lantarki (Na jijiyoyi) an

lilliɓesu da abin rufewa - kamar yanda mu mu keyi a yanzu tare da wayoyin lantarki -, dan kada siginal ɗin lantarkin ta goce ko ya tozarta, ko su sa maka takuruwa.

G- Wutar lantarki tana kewayawa a gefen kwalfar gurtsu da saurin kilo mita dubu a sakwan, in ba haka bafa lalle da sun faɗa a cikin kwalfar gurtsun, da aikin karfin fizga tare da kwalfar gurtsu mai wajabtawa, kuma da kasantacce ya rushe tun kafin ya fara, wannan itace saurin abin misali ga yanayin ƙwayar komayya.

H- Yayin da ƙwayoyin Haidurojin (Hydrogen) guda biyu suka haɗu to 0.007 % daga tattaran Haidurojin din suna juyawa zuwa makamashi, da ace waɗan nan nauyin sune 0.006 % maimakon 0.007 % to cewa Proton (Wata ƙwayace da ake samu a cikin ƙwayar komayya mai ɗauke da alamar + na cajin lantarki) bazai haɗu da Neutron ba (Wata ƙwayace da ake samu a cikin ƙwayar komayya da ba ta ɗauke da wata alama ta cajin lantarki), da kasantacce ya gushe tsantsar haidurojin kawai, to da kuma ragowar sinadaran basu bayyana ba, kuma da ace nauyin waɗanda suka juya zuwa makamashin sune 0.008 % a maimakon 0.007 % to da haɗuwar ta wayi gari da gaggawa sosai, al'amarin da zai kai zuwa ɓoyuwar Haidurojin din da gaggawa daga kasantacce, sai rayuwa ta koru tare da shi, to lambar yana lazimta ta zama tsakanin 0.006 % da 0.008 %.

I- Nauyin Electron (Wata ƙwaya ce da ake samu a cikin ƙwayar komayya mai ɗauke da alamar- na cajin lantarki), sun misalta 0.2 % daga nauyin Neutron, wannan itace ma'auni na nauyi dan samuwar da ƙwayar komayyar.

J- Furanni suna fuskanta bayan tsirowa kai tsaye daura da inda hasken yake futowa, tushen tsirran suna fuskanta wajen ƙasa yayin da furannin suke ni'imtuwa da ƙarfi mai yawa ga hasken, dukkan bayanan da suke buƙatar su dan tsayuwa da aikinsu ana samun su a lulluɓe ta cikin irin, akwai Hormones (Sanadaran da suke bada tasiri ga halitta) da suke

sarrafa ƙarin girma na tsawo da na faɗi ga tsirrai, da kuma fuskantar tushe, kuma dukkaninsu a lulluɓe suke a cikin iri.

L- Yayin da kai kake cin kayan marmari, masu daɗi sannan ka jefar da bushashshen ƙwayar iri mara ɗanɗano nesa da kai, kai da wannan kana bada dama ga waɗancan kayan marmarin da su shuɗar da ƙwayoyin halittun gadan su, ta yadda kayan marmari zasu baka ɗanɗano mai daɗi, a yayin da suke ɓoye ƙwayoyin halittar gadonsu - asalin rayuwarsu - acikin juyar da bushashshen ƙwayar iri mara tsiro, ba mai ruɗar da kai ba, baka kai ga jefar da waɗan nan iri ba akan ƙasa, har sai sun fara yayin da yanayi mai dacewa ya samu fitar da wata bishiyar kayan marmari da abinda ke cikinta na rassa da kututture, dukkanin wannan yana faruwa a cikin 'ya'yan itatuwa baka kiyaye komai.

N- Wanene wanda ya kiyaye bayanai ga waɗancan kayan marmarin, bebaye kurame, ya kuma kiyaye gwargwadan sukari dasu, ta yanda zasu ƙayatar da kai ?

Sannan: waye wanda ya sanya ƙwayar irin abar karɓa ba, kuma ba mai daɗi ba, har ka guje mata ka jefar da ita nesa da kai?

Sannan; Waye wanda ya cika ƙwayar irin da bayanai na gado isassu dan ta haifar da wasu tsirrai sababbi da dukkanin rabe-rabensu da ayyukan su?

M- Ya bayyana agare mu a ƙarshe cewa : Taƙaituwar zati ko taƙaituwar zati a wuri ɗaya ko a motsi iri ɗaya (Wani hali na zati da yake sanya shi ya taƙaita a waje ɗaya ko motsi iri ɗaya) waɗanda muke rayuwa acikin ni'imar ta itace samuwar nauyin kasantacce kamar abu ɗaya.

Me ake nufi da taƙaituwar zati ?

Da ace kai zaka hau mota katsahan sai motar ta tsaya, mai zai faru ?

Zaka yi gaba ne ! ko ba haka ba ne ?

Wannan shine abinda yake sa taƙaituwar zati (wato ƙoƙarin motsa jiki mara motsi dan yayi motsi) a wuri ɗaya ko a motsi iri ɗaya, ko taƙaituwar zati.

Da ace taƙaituwar zati (wato ƙoƙarin motsa jiki mara motsi dan yayi motsi) ya kasance a duniyar mu ƙasa da yanda yake akansa yanzu, da tashin iska mafi sauƙi na iya motsa kuramen duwatsu, acikin duniya kamar wannan zamu zama ababen bijirowa ko da yaushe ga kai harin kowane nau'ikan abubuwa !

Da ace abinda yake sa taƙaituwar zati a wuri ɗaya ko a motsi iri ɗaya ya kasance mafi girma daga yanda yake akan sa a yanzu da bamu samu ikon motsa 'yan yatsunmu ba.[2]

Kuma ƙarfin taƙaituwar zati ko abin da kesa taƙaituwar zati a wuri ɗaya ko a motsi iri ɗaya suna tsayawa akan dandazo.

Al'amarin da ya ɗimautar da masana Pysics (ilimin sanin ɗabi,a, cewa gungun taurari Milk way (Curewar dukkan taurari da kura da gas a wani tsari mai kama da zagaye idan za'a kalleshi daga sama) gungun taurarin da take ɗauke da tsarin hasken rana, baya tarayya a kiyaye taƙaituwar zati a wuri ɗaya sai da kaso 0.1 a Miliyan, a yayin da nauyin ƙasa baya kiyaye taƙaituwar zati a wuri ɗaya sai da kaso 0.001 a Miliyan.

Cikakkiyar taƙaituwar zati ko tsayuwar sa, a wuri ɗaya wacce muke rayuwa ta dalilin ta, wacce ta hanayar ta ne muke aiwatar da dukkanin ayyukanmu, itace sakamakon jumlar kuzarin kasantacce kamar abu ɗaya.

---

2 Nature's Destini: How the laws of Biology Reveal Purpose in the Universe, Michael Denton

{Kuma ba Mu halitta sama da ƙasã da abin da ke a tsakãninsu ba a kan ƙarya. Wannan shĩ ne zaton waɗanda suka kãfirta. To, bone ya tabbata ga waɗanda suka kãfirta daga wutã} {27}. [Surat Saad: 27].

Duk lokacin da ilimi ya yalwata, sai abubuwan mamaki na hikima da zirfafan halitta su bayyana! [3]

O- Sannan menene da mun tafi ga ido :

Waccan ni'imar da baza'a iya ƙaddara gwargwadan ta da kuɗi ba

﴿أَلَمۡ نَجۡعَل لَّهُۥ عَيۡنَيۡنِ ٨﴾ [البلد: 8]

{Shin bamu sanya masa idanuwa biyu ba} {8}. [Surat Al-Balad: 8].

Daidaiton gani na ido yana daidai da: Mega Pixel (Ma'auni ne da ake auna ƙarfin gani) ɗari biyar da saba'in.

Ido yana ƙunshe da mafi tsarkakar ƙwaya (ƙwayar ido) a duniya.

Kuma girman mai karɓar haske a cikin Retina (wani ɓangare na ido da yake canja hasken da ya shiga cikin ido zuwa signar lantarki wadda zai maida shi zuwa ƙwaƙwalwa dan samar da riska ta gani) faɗinsa baya wuce rabin ma'aunin murabba'in Millimeters (mm2), yana banbancewa da ita a tsakanin darajar launi miliyan goma da mafi nisansu mabambamta, lallai shi gajiayarwa ne da halittar Ubangiji mai ƙayatarwa.

Yayin da kake duba ga wani abu a gabanka, kuma haske yana sauka akan Retina, to cewa shi waɗansu matakai masu yawa na kimiyya, masu

3 Michael Denton ya tattauna wannan mas'alar a rarrabe acikin littafin sa:

Gwargwadan ɗabi'a, littafin an fassara shi na yaɗawar Darul Katib ne.

ƙulli, waɗanda a ƙarshe suke haifar da tafiyar lantarki mai ɗauke da caji (a ido) wannan tafiyar yana ciratarwa daga Retinar zuwa ƙwaƙwalwar ka, ta hanyar wayoyin jijiya, ƙwaƙwalwa a nan tana tsayawa da fassara kai kawon wannan ciratar wutar lantarkin mai caji akan cewa shine gani, kamar ƙwaƙwalwar tana mallakar wani ƙamus cikakke abin rigaya, yana maida ciratar wutar lantarkin mai ɗauke da caji wanda ya sadu zuwa gare shi zuwa wani ganin abin da ke gaban ka.

Wani abu mai ɗimautarwa, da kunyi tinani akan sa !

Ka riya : Wannan ƙwaƙwalwa, da take yanƙwanewa acikin akwatin ƙashi mai duhu - akwatin mai duhu shine mahaɗar ƙeya da kai -.

Babu mai saduwa da ƙwaƙwalwar ka sai ciratar ƙarfin wutar lantarki.

To ta yaya ƙwaƙwalwar take iya fassara wannan ciratar akan cewa shine gani?

Ta yaya ya baka gani ?

Wannan gajiyawar tana faruwane a lokaci ɗaya da zarar ka buɗe idanuwan ka, kayi duba !

Haka al'amarin yake dangane da ji :

Yayin da ƙararrakin sauti suke shiga zuwa gangar kunnenka, sai gangar kunnen ya juyar dasu daga ƙararrakin sautin zuwa wani motsi irin na inji, sannan wannan motsin na inji ya cirata ta hanyar ƙasusuwa uku kananu sosai acikin kunnen na tsakiya zuwa kunne na ciki wanda zai juyar da ita zuwa tafiyar lantarki mai ɗauke da caji.

Wannan ciratar na ƙarfin wutar lantarki, zai cirato a yanzu, daga kunne na ciki zuwa ƙwaƙwalwa, dan ƙwaƙwalwar ta fara rarrabe ciratar ƙarfin wutar lantarkin, zuwa wasu sautukan sai kaji sauti !

Dukkanin wannan yana gudana ne kuma a mafi ƙaranci daga wani yanki na sakwan

﴿وَٱللَّهُ أَخۡرَجَكُم مِّنۢ بُطُونِ أُمَّهَٰتِكُمۡ لَا تَعۡلَمُونَ شَيۡـٔٗا وَجَعَلَ لَكُمُ ٱلسَّمۡعَ وَٱلۡأَبۡصَٰرَ وَٱلۡأَفۡـِٔدَةَ لَعَلَّكُمۡ تَشۡكُرُونَ ٧٨﴾ [النحل: 78]

{Allah ne ya fitar daku daga cikkunan iyayenku baku sanin komai, kuma ya sanya muku ji da gani da zuciya wataƙila ku zaku gode masa} {78}. [Surat Al-Nahl : 78].

Ka riya cewa ƙwaƙwalwa dubbanan siginar lantarki suna saduwa zuwa gare shi, daga ido da kunne da shafa da ɗanɗano, daga kuma gaɓɓan jiki mabambanta, dan ya rarrabe tsakanin dukkan waɗan nan siginar ɗin da kyau, yana daga mafi mamakin abin da yake kasancewa.

﴿هَٰذَا خَلۡقُ ٱللَّهِ فَأَرُونِي مَاذَا خَلَقَ ٱلَّذِينَ مِن دُونِهِۦۚ بَلِ ٱلظَّٰلِمُونَ فِي ضَلَٰلٖ مُّبِينٖ ١١﴾ [لقمان: 11]

{Wannan shĩ ne halittar Allah. To ku nũna mini, "Mẽne ne waɗanan da ba Shi ba suka halitta? Ã'a, azzalumai sunã a cikin ɓata bayyananna} {11}. [Surat Luƙman : 11].

﴿وَتَرَى ٱلۡجِبَالَ تَحۡسَبُهَا جَامِدَةٗ وَهِيَ تَمُرُّ مَرَّ ٱلسَّحَابِۚ صُنۡعَ ٱللَّهِ ٱلَّذِيٓ أَتۡقَنَ كُلَّ شَيۡءٍۚ إِنَّهُۥ خَبِيرُۢ بِمَا تَفۡعَلُونَ ٨٨﴾ [النمل: 88]

{Aikin Allah ne wanda ya kyautata kowane abu lallai cewa shi masanine da abinda kuke aikatawa} {88}. [Surat Al-Naml: 88].

Waye zai iya kiyaye wata ni'ima ɗaya daga ni'imomin Allah?

Kayi tinani a cikin kowace gaɓa a cikin jikin ka, kuma acikin kowane ƙashi da suke baka damar motsi da gwargwadan su!

Kayi tinani a cikin gaɓɓai masu laushi, waɗanda suke baka damar motsi, ba tare da gogayya ba tsakanin kashi, ba tare da gurjewa ba, waɗan nan gaɓoɓin waɗanda Allah ya sanya maiƙo a cikinsu kamar kitse, wanda ake sanyawa a cikin gaɓuɓuwan injina!

Kayi tinani acikin ni'imomin Allah, kana mai lura kana mai godiya ga ni'imomin sa - tsarki ya tabbatar maSa -.

Ni'imomin Allah basa ƙirguwa

﴿أَلَمْ تَرَوْا۟ أَنَّ ٱللَّهَ سَخَّرَ لَكُم مَّا فِى ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِى ٱلْأَرْضِ وَأَسْبَغَ عَلَيْكُمْ نِعَمَهُۥ ظَٰهِرَةً وَبَاطِنَةً ۗ وَمِنَ ٱلنَّاسِ مَن يُجَٰدِلُ فِى ٱللَّهِ بِغَيْرِ عِلْمٍ وَلَا هُدًى وَلَا كِتَٰبٍ مُّنِيرٍ ﴿٢٠﴾﴾ [لقمان: 20]

{Ashe, ba ku gani ba, cẽwa Allah Yã hõre muku abin da ke a cikin sammai da abin da ke a cikin ƙasã, kuma Ya zuba ni'imõminsa a kanku, bayyanannu da ɓõyayyu ? Kuma akwai daga mutãne wanda ke yin jidãli ga al'amarin Allah, bã da wani ilmi ba, kuma bã da wata shiriya ba, kumã ba da wani littãfi mai haskakãwa ba} {20}. [Surat Luƙman : 20].

8- Wasu daga ciin masu musanta samuwar Allah yana sukar dalilin kulawa sai yace ai anan akwai wasu abubuwa waɗanda ba na misaliyya bane (Wata matafiyace ta falsafa da take sanya tinani mai bi da suranta abu a tinani), misali : Rashin lafiyoyi da girgizar ƙasa ?

Amsa : Rashin samun wasu abubuwa ababen kyautatawa a kasantacce a bisa iyakar bayanin mulhidi baya kore samuwar kautatawa.

Shi da hakan yana ƙarfafa, samuwar kyautatawa a cikin duniya.

In da ace a can babu kyautatawa tun asali, da muhidi bai riski samuwar wasu abubuwa ba ababen kyautatawa ba.

To ta yaya zaka din ga magana, game da wani aibi acikin tsarawa a cikin duniya ba tare da tsarin ba?

Amma abinda suke siffanta shi da cewa shi ba abin kyautatawa bane, to wannan taƙaituwa ne a ilimi, ko taƙaituwa a riskar hikima, daga abubuwa.

Muminai basa faɗin cewa kasantacce abin kyautatawa ne, dan haka masibu baza su afku acikinsa ba, kawai suna cewa lallai cewa: Kasantacce abin kyautatawa ne, dan haka wani abu bazai afku acikinsa ba batare da wata manufa ba.

Matsayar mulhidi mai kamanceceniya ne da wanda yake kore kyautatawa daga kumbo (wani inji da yake tashi ya ratsa sararin samaniya) dan samuwar wani gwargwado mai girma, daga sanadaran fetir acikinsa, wacce zata iya tarwatsa kumbon a kowane ƙifatawr ido[4]

Duniya ba'a tsarata ba dan ta zama duniya ta har abada, ko mara farko, mu ma ba'a tsaramu ba dan mu zama iyayen giji bane?

ba haka ba, mu ababen tsarawane dan a jarrabamu da alheri da sharri.

4 Zahirar sukar Addini a cikin falsafar zamani, na Dr. Sulɗan al-Umari, rubutu ne dan samun shaidar Digiri na uku.

﴿وَمَآ أَرۡسَلۡنَا مِن قَبۡلِكَ مِن رَّسُولٍ إِلَّا نُوحِيٓ إِلَيۡهِ أَنَّهُۥ لَآ إِلَٰهَ إِلَّآ أَنَا۠ فَٱعۡبُدُونِ ٢٥﴾ [الأنبياء: 25]

{Kuma muna jarrabarku da sharri da alheri domin fitina, kuma garemu zaku koma} {25}. [Surat Al-Anbiya: 25].

Alheri da sharri, da kowace fitina, suna kewayowane a fagen hikima da abinda Ubangiji Ya so.

9- Me zai hana ya kasance anan akwai wani dalili na madda, da ya samar da kasantacce, misali akan haka: Wata wayewa daban ko wani abu daban? Dan me yasa Ubangijin tun fil azal a iyakancewa?

Amsa: Anan akwa wata ƙa'idah wacee malaman Musulunci suka tabbatar da ita tun sama da shekara dubu a misali, wannan ƙa'idar tana cewa lallai cewa: "Tasalsul (Jerantuwa kamar daga wannan sai wannan sai wannan har zuwa rashin ƙarshe) a cikin masu aiki, yana kaiwa a larura zuwa rashin afkuwar ayyuka"[5]

Tasalsul (jerantuwa) acikin masu aiki wato: Samun mafi yawa daga mahalicci, acikin wannan tambayar, a wurinmu akwai wani cigaban (wayewa) daban da wani cigaban da ya rigayeshi da ya haifar da shi, da wani cigaban daya rigayesu ya kuma haifar da su haka nan, to wannan shine Tasalsul a cikin masu halitta.

Wannan Tasalsun ɗin yana kaiwa da larura zuwa rashin afkuwar ayyuka.

---

5 Zahirar sukar Addini a cikin falsafar zamani, na Dr. Sulɗan Al-Umari, rubune dan samun shaidar Digiri na uku.

Rashin afkuwar ayyuka wato: Rashin bayyanar ababen halitta misalin kasantacce da mutum da wasunsu.

To Tasalsul a cikin masu aiki yana kaiwa zuwa rashin bayyanar kasantacce da samuwa.

Da ace ɗaya daga cigaba (wayewa) bayyanar sa yana tsayawa akan wani cigaban daban daya farar da shi, ɗaya cigaban bayyanar sa yana tsayawa akan wani cigaban da ya rigaye shi akansa ya kuma farar da shi, hakanan har zuwa inda babu ƙarshe, wannan cigaban bazai bayyana ba ko wanda ya rigaye shi ko kuma waɗanda suka rigaye su, kuma samuwa ko kowane abu daban bazai bayyan ba.

Domin cewa kowane cigaba bayyanar sa tana tsayawa ne akan cigaban daya rigaye shi, haka nan bayan nan ba wani cigaba da zai bayyana, kuma da wani abu bazai bayyan ba.

To babu makawa daga wani Mahalicci a farko mara farko da Ya samar da kowane abu!

Da Tsalsul ya kasance babu ƙarshe, kuma kowane kewaye acikin sarƙar, yana dogarane akan wande ke gaban sa, to da ba'a samar da ababen halitta ko halitta ko samammu ba, domin mai aiki samuwar sa zai tsaya ne akan wani mai aiki da zai rigaye shi, kuma wanda ya rigayeshin yana tsayawane akan wanda ya rigayesu haka nan, bayan nan baza'a samar da kowane abu ba.

To babu makawa da sarƙar ta tsaya a wani iyaka.

A nan zamu ƙudire a yanke da Mahalicci na farko wanda wani abu bai rigayeShi ba!

10- Mu muna sanin ƙa'idojin da suke hukunta kasantacce, kuma muna sanin sabibin girgizar ƙasa sosai, to saboda me muke buƙatuwa zuwa mahalicci tunda mun san ƙa'idojin?

Amsa: Mulhidi yana ƙaddara cewa ƙa'idojin suna isa ga halittar kasantacce da bayyanar sa, haƙiƙa wasu daga mulhidai sun dogara akan tunanin "Dokokin fizgegeniya (Su wasu zahira ne na ɗabi'a wanda motsa kowane abu da karkatar sa yake cika ta hanyar sa daga ciki akwai taurari har haske)" kuma cewa shi ya isa dan bayyanar kasantacce, ba tare da duban faduwar wannan riyawar ba, da zarar tinani a cikin ainihin ƙanunul Jazibiyya, ko wanene yasa ƙa'idojin, ko wanene ya bashi siffar shiga da bayyanar da gurbi?

ba tare da duban waɗan nan bayyananun abubuwa na farko to lallai cewa dokar gravity (wani ƙarfi da yake sanya abubuwa suke jawuwa zuwa ƙasa ko junan su) baya kaiwa zuwa murgina ƙwallan bilyad (billiard).

To ƙa'idar ita kaɗai gajiyyaiyace daga kowane abu ba tare da bayyanar abun ba.

To gravity bai samar da ita bilyad ɗin ba, kaɗai yana motsata ne, idan ta bayyana aka kuma bugeta da sandar bilyad ɗin.

To Kanun na Jazibiyya ba wani abune mai zaman kansa ba, kawai shi wata siffa ce ga faruwa na ɗabi'a.

kuma dokokin gravity, ba zai motsa bilyad ɗin ba tare da wani ƙarfi da za'a danna akan sandar bilyad ɗin ba ta kuma motsa ta, a nan kawai ƙwallon bilyad ɗin yana motsawa kuma gurbin dokikin gravity suna bayyana.

saidai mulhidi yana ƙaddara cewa samuwar dokar gravity tana isa ga halittar bilyad ɗin da kuma sandar bilyad ɗin da kuma murginar ƙwallon!

To a cikin su biyun wannene mafi kusanci daga hankali ko mafurta a cikin dalilin bayyanar wannan kasantaccen: Shin Mahaliccin ne ko dokar?

Misali ƙanunun na ƙonewa ta ciki, a cikin injin mota bazata taɓa halittar injin motar ba.

Da ace mun raɓa ƙa'idojin ƙonewa na ciki, zuwa injin mota to lallai cewa injin bazai yi aiki ba, to babu makawa daga fetur, wanda zai bada dama, babu makawa daga tartsatsin ƙonewa, kuma babu makawa kafin hakan daga samuwar injin, to anan ɗa'idojin ƙonewa na ciki zasu bayyana suyi aiki a injin!

A hankali babu wani ƙaddarawar cewa ƙa'idojin ƙonewa na ciki suna isuwa dan halittar injin da tartsatsin ƙonewar da fetur da direban da hanya.

To tunanin isuwa da doka, dan fassara bayyanar kasantacce, ita fikirace bata dangantuwa ga hankali a cikin kowane abu.

Sannan lallai cewa wannan fikirar, da ace mun ƙaddarata to zata shigar damu a cikin jerantuwar ta masu aiki, wanda muka yi bayanin sa acikin amsa tambayar da ta gabata, to waye ya halicci wannan ƙa'idar, kuma wanene ya samar da ita, da sun riya cewa ita wata ƙa'idar ce daban to da mun shiga a cikin jerantuwar ta masu aiki, wanda yake hukunta rashin bayyanar kowacce ƙa'ida ko kowane abin samuwa.

11- Mai zai hana da ya kasance mafarar kasantacce shine bijirowar katsahan?

Amsa: Faɗa da katsahan shi jahiltar tushen ƙaddarawa ne؛ domin cewa ita katsahan, tana da sharuɗɗa guda biyu waɗanda baza su rabu da ita ba.

Sune: Zamani da guri.

Bijirowa katsahan tana sharɗanta wani zamanin da zata tabbata acikin sa, da farar da gurbin ta.

Kuma tana sharɗanta madda ta wuri da zata tabbata acikin sa, ta hanyar fitar da abin aikatawar ta.

To ta yaya zamu ce da wani ƙoƙari ga bijirowa katsahan acikin samar da kasantacce, tare da cewa kasancewar mu yazo daga rashin zamani da rashin guri ?

Kuma ta yaya gurbin katsahan zai bayyana ba tare da katsahan ɗin ba ita kanta ba ?

Kuma ta yaya katsahan zata bada wani gurbi kafin kasancewar ta, kuma samuwar zamani da samuwar guri waɗanda sune sharuɗɗa biyu na bijirowa katsahan na asali ?

12- Ta yaya zamuyiwa Mulhidi raddi, wanda yake cewa kasantacce bashi da farko ?

Amsa : Dacewa da doka ta biyu ta Thermodynamic (karantar kimiyya da ta alaƙantu tsakanin zafi da aiki da motsi) yana kore kasantacce ya kasance bashi da farko.

Dan bayyana wannan dokar ɗin, zamu buga wannan misalin dan yin bayanin sa ; Da ace a gurin ka akwai kofin ruwa tafasasshe aciki ɗaki, to lallai cewa zafin zai cirata daga tafasasshen ruwan zuwa yanayin ɗakin, har darajar zafin ɗakin tayi daidai da darajar zafin kofin, wannan shine doka ta biyu ta Thermodynamic, yayin da makamashi yake nasuwa daga sama zuwa ƙasa tsawon lokaci.

Wannan dokar ɗin yana faruwane a cikin kowane abu a cikin kasantacce kuma akowane ƙiftawar ido tun daga bayyanar kasantacce, har sai zafin kowane abu yayi daidai da kowane abu acikin kasantacce, yayin da zafin kowane abu yayi daidai acikin kasantacce daga abinda ake kira da : Mutuwar zafi ga kasantacce (Kasantacce bashi da wani yanayi na rashin tsarin alaƙar zafi da aiki da motsi) zai faru. Da ace kasantacce ya kasance bashi da farko to da abin ƙaddarawa shine ya wayi gari abin

tsayawa a yanzu - a mace dan zafi -, sai dai abinda yake a aikace cewa kasantacce a yanzu yana cikin hali mafi ƙaranci daga Maximum Entropy (yiwuwar yaɗuwar abinda yake bayyana ilimin da muke da shi a yanzu akan wani tsari shine wanda yafi girman adadin ƙarfi da bai kai adadin da za'ayi amfani dashi wajen aiki ba) bai kai ga mutuwar zafi ba bayan nan, a wannan lokacin shi bai zama mara farko ba, kai yana da farko matabbaci da zamani da guri suka bayyana tare da ita.

Haƙiƙa ya tabbata da cewa da ita kanta dokar ɗin cewa kasantacce ya fara wajen iyakar Minimum Entropy (mafi ƙaranci adadin ƙarfi da baikai adadin da za'ayi amfani da shi wajen aiki ba), wannan yana nufin cewa faruwar sa ta kasance akan wannan misalin daya gabata - abin ƙayatacce ne -.

Wannan shine ƙa'ida ta ilimi a wani ɓangaren, yayin da ilhadi yana wani ɓangaren daban tabbas.

13- Sabo da me ba'a ɗabbaka ƙannun na sababi (Babu makawa daga samun abubuwan da zasu kai zuwa sakamako, sai dai su basa farar da sakamakon da kansu) akan mahalicci ? ko da wata sigar daban : Waye ya halicci mahaliccin ?

Amsa : Da farko : Mahalicci ƙa'idojin ababen halittarsa basa ɗabbakuwa akansa wannan wani al'amari ne bayyananne.

In ba haka bafa da sai muce: Waye ya dafa mai dafa abinci?

Kuma wanene ya shafawa mai man mai?

Mahalicci a bayyane yake cewa Shi Mai samar da zamani ne da guri, dan haka ƙa'idojin basa ɗabbaƙuwa akan Sa, shine wanda Ya samar dasu - tsarki ya tabbatar masa -!

Na biyu:

﴿فَاطِرُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۚ جَعَلَ لَكُم مِّنۡ أَنفُسِكُمۡ أَزۡوَٰجٗا وَمِنَ ٱلۡأَنۡعَٰمِ أَزۡوَٰجٗا يَذۡرَؤُكُمۡ فِيهِۚ لَيۡسَ كَمِثۡلِهِۦ شَيۡءٞۖ وَهُوَ ٱلسَّمِيعُ ٱلۡبَصِيرُ ١١﴾ [الشورى: 11]

{Kowane abu fararre yana da wanda ya farar dashi, wannan ingantacce ne, sai dai Mahalicci. (Babu wani abunda yai kama da Shi} [Surat Al-Shura: 11]

Na uku: Mahalicci ba fararre bane - kai Shi bashi da farko - to ta yaya zamuce waye ya halicce Shi?

Na huɗu: Ba makawa da Mahalicci Ya zama bashi da farko, wajibnin samuwa, inba haka bafa da mun shiga acikin mushkilar "Tasalsul acikin masu aiki wanda da larura yake kaiwa zuwa rashin afkuwar ayyuka" wannan shine abinda mukayi bayanin sa kafin lokaci kaɗan a rarrabe, babu makawa da Mahalicci Ya zama mai wajibin samuwa tun farko mara farko - tsarki ya tabbatar maSa -.

14- Kasantacce mai girmane, to yaya zamu zama da yanayin giraman namu ƙarami ababan tabbatarwa a cikin wannan kasantaccen mai girma?

Amsa: Mulhidi yana sanya ƙaddarawa tauyayye sai yace: Duk da cewa kasantacce mai girma ne, a wannan lokacin, mutum ba ginshiƙi bane a cikin wannan kasantaccen.

Wannan ƙaddarawar, abin ginawa ne akan wata Muƙaddima: Duk da cewa gonar mai faɗi ce sosai amma mai ita jikin sa ƙarami ne sosai, inka danganta da ita a wannan lokacin: Shi ba mai ita bane!

Al'amarin ba wai da girman jiki bane kai tsaye.

Dabi'un da suke babu wani girman jiki na madda, sune ma'auni mafi girma a cikin fifitawa tsakanin mafi girman mutane da mafi ƙaskancin mutane.

Mutane ana auna su ne da ɗabi'unsu.

To mas'alar girma ba sune ma'auni ba!

Kubar mu, mu buga wannan misalin: Da ace a wurin mu akwai wani sarki ,wannan sarkin yayiwa ɗansa wasiyya da wasu daga wasiyyoyi, da nasihohi, ya rubuta masa littafi a kan haka, shin zai yiwu ga wani mai tawaye yazo yace: Ta yaya a samu wannan sarkin ya mallaki miliyoyin fadojin nan da filayen nan masu faɗi, waɗanda babu iyaka gare su, da ya bada muhimmanci (kulawa) ga ɗansa wannan wanda girman jikin sa da nauyin sa, basu kai ɗaya bisa miliyan ba, ta yanda zai mallaki wannan mulkin na filaye da fadoji?

Misali mafi ɗaukaka ya tabbata ga Allah.

Shin wannan tawayen (bijirewa) abin hankaltuwa ne tun asali?

Al'amarin bai zamo da girman jiki ba ko da awo.

Kuma sannan shin wannan kasantaccen bai fara daga ɗigon maniyyi mafi ƙanƙanta daga kan kusa da biliyoyi, kamar yanda kowane masanin Physics yake tabbatarwa ba?

Idan hakane girman jikin na dangantaka ne.

Sannan me yake cutar da mulhidi cewa Allah Yana halittar abin da yake so ta yanda Yake so?

Shin Ubangiji yana fama ne da tawaya, acikin abubuwan da suke shigowa, har ya ciyar da gwargwadan buƙata?

Allah Ya ɗaukaka game da hakan.

Sai dai shin a aikace muna misalta wani ginshiƙi a cikin wannan kasantaccen?

Eh kai ya kai mutum: ginshiƙin wannan kasantaccen da taklifi na Ubangiji.

Taklifi na Ubangiji shine: Addini.

Addini shine amanar da ka ɗauke ta, shine jarrabawa mafi girma, wanda kai abin nema ne da bada shi.

Kai ya kai mutum abin nemane da bauta ga Allah - maɗaukakin sarki -, da wannan ne za ka zama abin cusawa a cikin wannan kasantaccen, kai ginshiƙin wannan kasantaccen ne bada girman jikinka ba ba kuma da ƙarfin ka ba kuma bada ikon ka ba kadai da taklifi na Ubangiji.

Kai ne mai iko ne abisa aikata alheri da barin sharri ... mai iko akan imani da kafirci.

Dukkanin mu yana sanin cewa shi abin ɗorawa shari'a ne daidai ne mun so ko mun ƙi!

Mulhidi da mumini da wanda ban sani ba, kowa yana sanin cewa shi abin ɗorawa shari'a ne, kuma yana jin taklifin Ubangiji, kuma yana fama da raɗaɗi na rai, yayin fahimtar sa da cewa abin da yayi mai munanawa ne na ɗabi'u, yana sanin cewa a tare da shi (akwai karɓar umarnin) ka aikata ko (hanin) kada ka aikata, aikata alkhairi, kada ka aikata sharri, kuma ya sani a kansa cewa shi abin nema ne!

Mu muna cikin cusawar wannan kasantaccen a taklifanci (Dora shari'a).

Kuma dai mu muna cikin ginshiƙin wannan kasantaccen ta riska da sani, mu muna riska muna kiyayewa muna hankalta, kuma muna sanin haƙiƙar samuwar mu da kuma haƙiƙar kasantacce a gefan mu, kuma muna fahimtar samuwar mu sosai.

Mu ababen nema ne, ababen kamu,ababan ɗorawa shari'a, ababen yiwa hisabi.

Mu mai kasancewa mai riska ga tsoron tanadi da kulawa, mu mai kasacewa ne mai riska ga kyautatawa, mu mai kasancewa ne mai iko akan zartar da abinda aka ɗora masa shi ko kafircewa da abin da aka ɗora masa, mu muna da iko sosai akan jarrabawa, mu muna da iko akan imani da kafirci.

Mu muna cikin ginshiƙin wannan kasantaccen.

﴿إِنَّا عَرَضْنَا ٱلْأَمَانَةَ عَلَى ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ وَٱلْجِبَالِ فَأَبَيْنَ أَن يَحْمِلْنَهَا وَأَشْفَقْنَ مِنْهَا وَحَمَلَهَا ٱلْإِنسَٰنُ ۖ إِنَّهُۥ كَانَ ظَلُومًا جَهُولًا ٧٢﴾ [الأحزاب: 72]

{Lalle Mũ, Mun gitta amãna ga sammai da ƙasã da duwãtsu, sai suka ƙi ɗaukarta kuma sukaji tsõro daga gare ta, kuma mutum ya ɗauke ta, lalle shĩ (mutum) ya kasance mai yawan zãlunci, mai yawan jãhilci} {72}. [Surat Al-Ahzab : 72].

15-Wasu daga cikin Mulhidai suna cewa : Ana samun da yawa daga taurari, bayan nan a binciken ƙaddarawa, yana daga ɗabi'a cewa yakasance anan akwai wani tauraro ga rayuwa... shin wannan kafa hujjar yana inganta ?

Amsa ; Menene alaƙar taurari masu yawa, da sukan dalilin kyautatawa ? Mas'alar bata zamo maddodi na farko ba.

Bai zamo cewa ni ina cikin wani daji mai cike da dukkanin korren shukoki da 'ya'yan itatuwa da dabbobi, ma'anar hakan bai zamo cewa ƙwaryar dafaffen abinci, abin sha'awa zata bayyana katsahan acikin tsakiyar dajin ba, mas'alar bata zamo maddodi na farko ba !

Kuma bai zamo ma'anar samuwar rairayi acikin hamadar duniya, ma'anar sa bai zamo cewa ni zan samu na'urori masu sarrafa lambobi da kuma ƙwaƙwalen injina masu aiki da lantarki waɗanda ake yinsu daga rairayi, a gefena a kowane wuri a cikin hamada !

Al'amarin ba wai maddodi ne na farko ba, al'amarin aiki ne da kyautatawa.

Bawai kawai samun wasu tattaren taurari bane, su zama sun isu da cewa wani tauraron ya bayyana da wannan kyautatawar kamar ƙasa.

Al'amarin kyautatawa ne da halitta da aiki.:

﴿وَتَرَى ٱلۡجِبَالَ تَحۡسَبُهَا جَامِدَةٗ وَهِيَ تَمُرُّ مَرَّ ٱلسَّحَابِۚ صُنۡعَ ٱللَّهِ ٱلَّذِيٓ أَتۡقَنَ كُلَّ شَيۡءٍۚ إِنَّهُۥ خَبِيرُۢ بِمَا تَفۡعَلُونَ ٨٨﴾ [النمل: 88]

{Aikin Allah ne wanda ya kyautata kowane abu} {88}. [Surat Al-Naml : 88].

Samun wasu taurarin daban masu yawa, baya kuɓutarwa a sake, samun wata rayuwar abisa tauraron ƙasa.

Samuwar wasu duniyoyin daban baya tabbatar da tsarin ƙwayoyin halitta a jikinka daga haruffa biliyan huɗu waɗanda suke sarrafa dukkan ayyukanka da gaɓɓanka da sanadaran da ke sarrafa halitta, da kiyayewa mai ƙayatarwa, tun kafin a same ka kai da kanka !

Rayuwa abar sanice ba wai madda bace.

Da ace zamu hau ni da ɗaya daga cikin mulhidai akan ɗaya daga duniyoyi, mu binciko wata na'ura mai rikitarwa wacce take aiki na ban mamaki, ko da bamu fahimci aikin sa ba bayan nan, shin zai yiwu a musanta wanda yayi wannan na'urar saboda kawai girman duniyar da mu muke akanta?

bayyana ta hankali, tana tunkuɗa mu, ni da mulhidi yayin da muka ga wannan na'ura dan faɗa da Mai samarwa kuma Mai iko.

Wanda yake musanta wannan bayyana ta hankali, wanda yake musun Mai samarwa shine abin nema da dalili ba wai mai tabbatarwa ba.

Mulhidi a cikin wannan kasantaccen mai ban mmaki mai kyau, shine abin nema da dalili, ba wai mumini ba !

Wani lokaci mulhidi (Mai aƙidar) bansan cewa akwai Allah ko babu ba, shine Carl Sagan ya rubuta wata riwaya sunanta " Contact", yana hakaitowa acikinta cewa ta yaya malamai suke bincike game da basira a wajen kasa.

A cikin riwayar ta riyawa malamai sun gano wata sarƙa mai tsawo daga lambobi na farko mai gabatowa daga sararin waje؛ domin cewa wannan jerantuwa ta farko tana fa'idantar da wata ƙima ta horarwa abar iyakancewa, wata ƙima ce da take nuni akan wani nau'i na kiyayewa, sai wannan ya zama wani dalili na hankali mai isa dan su yarda a yanke cewa wannan saƙon mai gabatowa ne daga wani cigaban daban da yake ƙoƙarin saduwa tare da mu !

Labari mai daɗi shine cewa Carl Sargan mai aƙidar bansani ba shin akwai Allah ko babu mashahuri, saidai hankalin sa yana miƙa wuya ga tabbacin cewa ƙulli da tsari, acikin wani saƙo ƙarami, shine dalili akan hujjar samarwa da kyautatawa !

Sarƙa kawai daga lambobi na farko zaka yarda a yanke da samuwar cigaba mai girma, to ta yaya zaka danganta harafi biliyan huɗu a cikin kowace sanadarin rayuwa (Itace sanadari ta tushe wacce kowane mai rai yake kasancewa daga gare ta) daga maddodin jikinka, waɗanda da wani harafi daga garesu ya ɓaci da wataƙila masifa ta faru, to ta yaya zaka danganta dukkan wannan kyautatawar zuwa yaudare-yaudaren ilhadi na rashin hankali ?

Baya zamowa daga hankali a cikin wani abu yarda da hukunci zuwa ga yaudare-yaudare, dan hana fassara mabayyana a fagenta na shiryarwa akan mahalicci

﴿قُلِ ٱنظُرُواْ مَاذَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۚ وَمَا تُغۡنِي ٱلۡأٓيَٰتُ وَٱلنُّذُرُ عَن قَوۡمٖ لَّا يُؤۡمِنُونَ ١٠١﴾ [يونس: 101]

{Ka ce : "Ku dũbi abin da yake cikin sammai da ƙasa."Kuma ãyõyi da gargaɗi bã su wadãtarwa ga mutãne waɗanda bã su yin ĩmãni.{101}. [Surat Yunus : 101].

16- Me yasa bai zamo akwai sama da Mahalicci mara farko ba ?

Allah - maɗaukakin sarki - Ya ce :

﴿لَوۡ كَانَ فِيهِمَآ ءَالِهَةٌ إِلَّا ٱللَّهُ لَفَسَدَتَاۚ فَسُبۡحَٰنَ ٱللَّهِ رَبِّ ٱلۡعَرۡشِ عَمَّا يَصِفُونَ ٢٢﴾ [الأنبياء: 22]

{Da ace a cikinsu akwai wasu ababen bautar ba Allah ba to da sun baci} {22} [Surat Al-Anbiya: 22].

Samuwar wani abin bautar tare da Allah yana hukunta gididdiguwa (yawaita), kididdiguwa tana lazimtar da buƙatuwa.

Buƙatuwa ga Mahalicci - tsarki ya tabbatar maSa yana lazimtar rashin amintar da kasantacce, kuma cewa shi zai fadi...yana lazimtar ɓacin kasantacce.

Babu lamuni ga wanzuwar kasantacce tare da wani abin bauta mai buƙatuwa!

﴿لَوۡ كَانَ فِيهِمَآ ءَالِهَةٌ إِلَّا ٱللَّهُ لَفَسَدَتَاۚ فَسُبۡحَٰنَ ٱللَّهِ رَبِّ ٱلۡعَرۡشِ عَمَّا يَصِفُونَ ٢٢﴾ [الأنبياء: 22]

{Dã waɗansu abũbuwan bautawa sun kasance a cikinsu (sama da ƙasa) fãce Allah, haƙĩƙa dã su biyun sun ɓãci. Sabõda haka tsarki ya tabbata ga Allah Ubangijin Al'arshi daga abin da suke siffantãwa} [Surat Al-Anbiya: 22].

Mahalicci Ya tsarkaka daga buƙata da buƙatuwa Shi Mawadaci ne tabbatacce da kanSa tsarki ya tabbatar maSa.

Ka ƙara ga abinda ya gabata: Lallai cewa shi da ace yakasance acikin su akwai ababen bautawa guda biyu ko sama da haka to yiwuwar karo shine mafi kusa a hankalce daga dacewa, domin mafi yawa daga abin bauta ɗaya yana nufin mafi yawa daga mashi'a da mafi yawa daga nufi, kuma ƙididdiguwar manufofi yana nufin buƙatuwar kowane ɗaya, wannan yana lazimtar ɓacin sammai da ƙasa.

Dabi'ar mutum da aka halicceshi akanta tana yarda ayanke da cewa Allah Shi kaɗai ne, da ace masanin Pysics ko wanin sa zasu yi duba a cikin wannan kasantaccen babu abinda zai suranta gare shi sai Mahalicci ɗaya to wannan itace ɗabi'ar da aka halicci mutum akanta.

17- Saboda me Addini?

Amsa: Mafi munin ɗabiar Mulhidi (Antony Garrard Netwoton Flew) yana imani da cewa gaskiya tafi ƙarya, shin ba haka bane?

Ashras Mulhidi yana imani da cewa, amana tafi ha'inci, shin ba haka bane?

Waɗan nan ma'anonin kalmomin, ba daga wannan duniyar bane, kuma a duniya ta madda babu abinda zai kuɓutar da ma'anar su, ko abinda suke hukuntawa.

Mene ne ma'anar gaskiya?

Menene ma’anar amana?

Shin da ace mun tsaya da bincika zirfafan ƙwayar komayya, shin za mu lura da ma'anoni misali: Gaskiya ko ƙarya?

Shin da ace za mu lura da tsarin kimiyyar taurari na ɓangaren abinda suka ƙunsa da motsin su a sararin Subhana ko kuma kimiyyar sanadaran dake sarrafa halitta za mu lura da: Amana ko ha'inci?

Waɗan nan wasu ma'anonin kalmomi ne ba daga wannan duniyar ta madda ba.

Sai dai su wasu ma'anonin kalmomi ne na haƙiƙa.

Kai su suna daga mafi girman al'amura.

Kimar mutum (tana tabbata) da ɗabi'un sa ne. Bada girman jikinsa na madda ba, kuma bada adadin ƙanƙantar sa bane, ba kuma da matsayin ikon sanadarin rayuwar sa bane.

Kimar mutum tana tabbata ne ta hanyar lazimtar sa da taklif na Ubangiji a cikin sa.

Wannan ƙimar wani abu baya tarayya acikin ta tare da mutum daga duniya ta madda.

Acan akwai wani mutum na gari da wani mutum ɓatacce.

Sai dai ba'a samun dutse na gari, da ɓataccen dutse.

Kuma bama lura da wani tauraro amintacce da tauraro maha'inci.

Mutum kawai shine abin nufi da ƙima, kuma abin nufi da manufa, kuma abin nufi da samuwa.

Mutum da Aljani kawai sune suke game fahimtar cewa shi abin ɗorawa shari'ane.

Ji da ma'anar ɗabi'u ba komai bane, sai wani yanki daga ɗabi'ar da aka halicci mutum akanta, ta taklifanci na Allah, acikin kowanne daga cikin mu.

Addini larura ne ga fahimtar mutum.

Addini shine ɗaya, wanda yake kuɓutar da ma'anar ɗabi'u, kuma saboda me suka samu, kuma saboda me muke jin larurar lazimtuwa da su.

Abu ɗaya wanda yake bawa ɗabi'u siffar su, shine Addini.

Dabi'u fahimtar su bata yiwuwa sai acikin fagen taklif na Ubangiji.

Kuma sanin me yasa su ɗabi'un da aka halicci mutum akansu, acikin jinsin mutum baya yiwuwa sai ta hanyar Addini.

Kuma ta hanyar Addini ne muke sanin manufar samuwa, muke kuma sanin cewa ɗabi'un da muke ji da larurar lazimtuwar su, koda bamu lazimta dasu ba, su wani yanki ne daga taklif na Allah.

Addini larura ne na mutum.

Ta hanyar Addini kuma muke sanin dan me yasa muke a nan?

Kuma muke sanin menene bayan mutuwa?

Muke sanin ma'anar samuwa.

Muke sanin menene abin nema daga gare mu a cikin wannan samuwar?

Addini tilas ne ga sanin mafi muhimmancin abinda yake shagaltar da mutum.

Sabo da haka da rashin Addini duniya gaba ɗayan ta take juyawa zuwa cikakken ɓata da cikakken rashi.

Ibnul Kayyim - Allah Yayi masa rahama - yana cewa; "Babu hanya zuwa arziƙi da rabauta, ba a duniya ko a lahira ba, saidai a hannun Manzanni, kuma babu hanya zuwa sanin tsattsarka da mummuna a rarrabe, sai ta ɓangaren su, kuma babu mai samun yardar Allah kwata-kwata sai a hannun su".[6]

Duniya mai duhuce abar la'anta, sai dai abin da ranar Addini da ranar Manzanci suka fito akansa kamar yanda babban malamin Musulunci IbnTaimiyya - Allah Yayi masa rahama - yake faɗa. [7]

Da rashin Addini ba'a sanin manufar samuwa ko ma'anar alheri ko ƙimarsa.

Da wanin saƙonni duniya zata canja zuwa Absurdism (Koƙarin mutum dan gano kasantacce ƙarshe ya ƙare da rashin nasara) mai tsoratarwa.

Lokacin da Addini yake ɓoyuwa, kuma mutum yake musun Annabta a lokacin ta, to mutum zai juya zuwa sharat taurari, kamar yanda Carl Sagan yake faɗa, da ƙwari kamar yanda Sartre (Shine Jean Paul Sartre) yake faɗa. [8]

---

6 Zadul Ma'ad 1-68.

7 Majmu'ul Fatawa 19-9394.

8 Tushem da aka samo bidiyo: The Shores of the Cosmic Ocean [Episode 1] Wasu sashi na halittar mu ya sani daga nan ne muka futo. Kuma muna marmarin dawowa, kuma zamu iya. Saboda sararin samaniya yana tare da mu. Mu anyimu ne daga kayan tauraro. Mu hanya ce ga sararin samaniyar ta san kanta. 06 min 04 sec. Amma

Mutum yana wayar gari a aikace dusa a kimiyya ko da ma'ana mafi zirfi datti a kimiyya, kamar yanda Stephan Hawking yake faɗa. [9]

Annabta itace bugun zuciyar samuwa mafi kaɗaita, batare da Annabta ba mafi ƙayatarwa daga ababen ƙirƙira da mafi daɗin sha'awe-sha'awe zasu canja zuwa tsoro!

Da rashin Addini, duniya zata canja da dukkanin kyanta zuwa fatalwoyi masu ban tsoro.

Kai da ka tambayi kowane mulhidi abisa kowace tambaya ta samuwa misali: Dan me yasa muke anan a cikin wannan duniyar ko menene bayan mutuwa?

Lallai cewa ko dai ya yaudarar da tambayarka, ko ya lazimci bebentaka cikakkiya.

A wannan lokacin Addini shine mahukuntar ɗabi'a ga fahimtar mutum da fahimtar larurar ƙimomin ɗabi'u, kuma tilas ne ga sanin samuwa da manufa daga samuwar, da tabbatar da bauta da Allah waccan bautar da tsira yake da ita.

18- Me zai hana waɗan nan ɗabi'un su zama sakamakon ƙwaƙwalwa ko abin al'umma?

Amsa: ƙwaƙwalwa tana haɗuwa daga ababen kasancewa na madda, waɗanda suke acikin duniyar madda dai-dai da dai-dai!

---

kasancewar mutum ƙwari to haƙiƙa Sartre ya ambata a cikin riwarsa Nausea (Littafi na labari wallafar Sartre).

9 Daga tattaunawa tare da Ken Campbell a (shirin) Reality on the Rocks: Beyond Our Ken (Haƙiƙanin lamari akan duwatsu nesa da hangen mu, 1995.

Aduk ta yadda ƙwaƙwalwa ta ƙullu, ko ababen hauhawarta na madda suka ƙullu, to tattaran ziruka bazai bada sakamkon komai ba sai zero!

Idan madda ta kasance bata sanin alheri ko sharri to ƙwaƙwalwa ma kamar haka take!

Anan zamu tambayi mulhidi: Ta yaya ma'anar alheri da sharri suka bayyana, idan duniyar madda gaba ɗayanta ta kasance mai karkacewa a ɗabi'u, kuma bai san alheri ko sharri ba?

Tamabaya ta biyu: Me zai hana hani na ƙwaƙwalwa daga halakar da mutanen ƙasa gaba ɗaya?

Kuma mezai hana hani na ƙwaƙwalwa daga shigar da asalin mutum na ƙasa tarkunan dabbobi?

Me zai hana hani na ƙwaƙwalwa daga halakar da marasa lafiya, da masu buƙata ta musamman, da gajiyayyu, da asalillika na ƙasa, kamar yanda ya faru a cikin mashru'i na wanzuwar fifiko da yawaita ga ɗaiɗaiku saboda saɓani a zahiri wanda Nazi yayi shi - Mashru'in Akshin ti fur -?[10]

Waɗan nan tambayoyin, ƙwaƙwalwa ta madda bata mallakar amsa game dasu da kuskurantarwa ko ingantawa.

Kwaƙwalwa mai kaucewa ce a cike daga ɓangaren ɗabi'u, domin cewa shi yana hauhawa daga ainihin ƙwayoyin komayya na ƙasa.

Babu wata alaƙa tsakanin ƙwaƙwalwa da ɗabi'u ko a kusa ko a nesa.

Amma tinanin cewa al'umma itace mafarar ɗabi'u, to wannan tinani ne baƙo, domin cewa ɗabi'u suna nufin mutum, kamar mutum ne kuma al'umma basu zama kamar al'umma ba.

10 https://en.wikipedia.org/Aktion-T4

Sannan lallai cewa al'umma itace ainihin ababen yin madda, bayan nan to taron zeruka wani karon daban bazai bayar da sakamakon komai ba sai zero, to ta yaya al'umma za ta bayar da sakamakon ɗabi'u, alhali su basa dangantuwa ga duniyar madda tun asali?

Sannan da ace wannan zancen ya inganta, mun ɗauki cewa ɗabi'u sune sakamakon al'umma to anan Nazi zai wayi gari abin zubawa acikin halakar wanin sa, domin al'umma suna ganin hakan.

Yayin da duniya ta tabbatar da hukunta Nazi, wannan rahota ya kasance ginine akan cewa ɗabi'u a sake suke, bawai sakamakon al'umma bane, inba haka bafa da hukunta Nazi bazai yiwuba, kuma basu fahimci cewa shi yayi kuskure ba tun farko!

Dabi'u masu zaman kansu ne daga al'umma, daidai to daidai ne a wurin al'umma ta gari, da kuma ɓatacciyar al'umma.

Kuskure kuskurene a wurin al'umma ta gari da ɓatacciyar al'umma.

To ɗabi'u suna da wata ma'ana da take wuce ƙwaƙwalwa da al'umma.

19- Ana samun mafi yawa daga Allah, a cigaban ƙasa, to dan me yasa za'ayi imani da Allah a iyakance?

Amsa: Ba'a samun wani abin bauta a cikin dukkanin Addinan dake bayan ƙasa sai Allah.

Saɓanin mu tare da ragowar Addinai cewa su, sun riƙi wasu ƙananan Allloli tare da Allah misalin Yasu'u da Ruhul-Kudus a cikin Kiristanci, da Shif da Barahima acikin Hundus...har zuwa ƙarshe.

Addinai dukkanin su suna imani da Allah shi kaɗai mafi kaɗaitaka, Shi a wurin su mahaliccin samuwa ne.

Saidai cewa su, suna sanya wasu Allolin daban tare da Allah.

Kai hatta gumakan mushrikai, basu kasance suna riƙon su iyayen giji ba akan kansu kawai sun kasance suna miƙa wuya cewa Allah shine Mahalicci sai dai cewa, su suna sanya su tsanuka ga Allah.

﴿وَلَئِن سَأَلۡتَهُم مَّنۡ خَلَقَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضَ وَسَخَّرَ ٱلشَّمۡسَ وَٱلۡقَمَرَ لَيَقُولُنَّ ٱللَّهُۖ فَأَنَّىٰ يُؤۡفَكُونَ ٦١﴾ [العنكبوت: 61]

{Lalle idan ka tambaye su: "Wãne ne ya halitta sammai da ƙasã kuma ya hõre rãnã da watã?" Lalle sunã cẽwa Allah ne. TO, yãya ake karkatar da su?} {61}. [Surat Al-Ankabut: 61]

Babban malamin Musulunci Ibn Taimiyya - Allah Yayi masa rahama - yana cewa: "Duk wanda yayi zatan cewa masu bautar gumaka sun kasance suna ƙudirce cewa su suna halittar talikai, ko cewa su suna saukar da ruwa, ko cewa su suna tsirar da tsirrai, ko suna halittar dabbobi ko makamancin wannan, to shi ya jahilce su, kai manufar masu bautar gumaka ta kasance ga gumakan su yana daga jinsin manufar mushrikai da ƙaburbura" [11]

Will Durant yana tabbatarwa cewa, asalin Addinin Hindu masu bautar gumaka, a ƙarshe suna komawa zuwa imani da Allah ɗaya mafi kaɗaita, sai yake cewa game da Allolin Hundus: "Waɗan nan dubunnan Allolin, sune irin abinda cocunan Kiristoci suke aikatawa na tsarkake dubbun rayuka tsarkakakku dan haka baya ɗarsuwa zuwa tinanin ɗan Addinin Hindu koda da ƙiftawar ido daya, cewa waɗan nan Allolin waɗanda babu taƙaituwa ga adadin su suna da shugabanci maɗaukaki"[12] .

11 Majmu'ul Fatawa 1 p 359.

12 Kissatul Hadara, Will Duranta, 3, p. 209.

Haƙiƙa rahoton da aka ɗaga zuwa hukumar England a cikin tsakiyar mulkin mallakar Englnd ga Indiya cewa: " Sakamako gamamme wanda kwamiti yakai ƙarshe zuwa gare shi na bincike shine cewa da yawa daga 'yan Indiya mafi rinjaye suna ƙudire Aƙida tabbatacciya a sha'anin Allah ɗaya mafi ɗaukaka". [13].

Allah ɗaya ne a cikin dukkanin Addinan dake bayan ƙasa.

﴿۞ وَلَا تُجَٰدِلُوٓاْ أَهۡلَ ٱلۡكِتَٰبِ إِلَّا بِٱلَّتِي هِيَ أَحۡسَنُ إِلَّا ٱلَّذِينَ ظَلَمُواْ مِنۡهُمۡۖ وَقُولُوٓاْ ءَامَنَّا بِٱلَّذِيٓ أُنزِلَ إِلَيۡنَا وَأُنزِلَ إِلَيۡكُمۡ وَإِلَٰهُنَا وَإِلَٰهُكُمۡ وَٰحِدٞ وَنَحۡنُ لَهُۥ مُسۡلِمُونَ ٤٦﴾ [العنكبوت: 46]

{Ubangijin mu da Ubangijinku ɗaya ne} [46]. [Surat Al-Ankabut : 46]

Amma gumaka da Allolin mutane basu zamo ba, sai tsanuka na kafirci ga Allah.

﴿أَلَا لِلَّهِ ٱلدِّينُ ٱلۡخَالِصُۚ وَٱلَّذِينَ ٱتَّخَذُواْ مِن دُونِهِۦٓ أَوۡلِيَآءَ مَا نَعۡبُدُهُمۡ إِلَّا لِيُقَرِّبُونَآ إِلَى ٱللَّهِ زُلۡفَىٰٓ إِنَّ ٱللَّهَ يَحۡكُمُ بَيۡنَهُمۡ فِي مَا هُمۡ فِيهِ يَخۡتَلِفُونَۗ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يَهۡدِي مَنۡ هُوَ كَٰذِبٞ كَفَّارٞ ٣﴾ [الزمر: 3]

{Waɗanda suka riƙi wasu majiɓinta, ba shi ba (Suna cewa) : " Bamu bauta musu ba face domin su kusan kusantar da mu zuwa ga Allah kusantar daraja} {3}. [Surat Al-Zumar : 3].

---

13 Littafin da ya gabata.

20- Idan mutum ya aikata wani abun da baya buƙatarsa hakan wasa ne ! Allah baya buƙatuwa zuwa gare mu, to dan me yasa ya halicce mu?

Amsa : Tunanin cewa buƙata wasa yana fuskantarta, shi tinani ne mai rauni!

Buƙata hikima ce take fuskantarta ba wai wasa ba.

Likita mai dukiya ma'abocin kyakykyawan ambato yakan yiwa mutane magani, ba tare da ya buƙaci wani abu daga gare su ba, kai yana yi musu magani dan maslahar su ne su, anan mu bama siffanta aikinsa da cewa shi wasa ne!

Hikima da manufa mai girma, suna daga bayan hankali, basa kewayewa acikin kewayen sarƙar buƙata/wasa.

Zai iya yiwuwa wani ɗaya daga masu iwo zai tsamo wani yaro dan tausayi gare shi, sannan ya barshi ya tafi, ba tare da sauraren wani yabo daga masu yaron ba, to anan aikin sa ba'a sannafa shi da cewa shi buƙata ne ko wasa, kai wannan aiki ne mai girma da manufa mai kyau da ɗabi'u masu tasrki!

Babu lazumtar juna tsakaknin buƙatu da wasa![14]

A cikin Sahihu Muslim, a cikin Hadisi Kudisi, Allah - maɗaukakin sarki - Ya ce: " Yaku bayi Na da ace na farkon ku da na ƙarshen ku da mutanen ku da Aljanin ku sun kasance abisa mafi tsoron Allah na zuciyar wani mutum ɗaya daga gare ku wannan bazai ƙara komai acikin mulkiNa ba, yaku bayiNa da ace na farkon ku dana ƙarshen ku da da Aljanin ku sun kasance abisa mafi fajircin wani mutum ɗaya, wannan bazai rage komai daga mulki Na ba, yaku bayiNa kaɗai sune ayyukan ku da Nake kiyaye su gare ku, sannan in cika muku su, wanda ya sami wani alheri, to ya

14 Zahirar sukar Addini a cikin falsafar zamani, na Dr. Sulɗan Al-Umari, rubune dan samun shaidar Digiri na uku.

godewa Allah, wanda ya sami wanin hakan, to kada ya zargi kowa sai kansa"[15]

To Allah Mawadaci ne daga talikai.

Kuma aikin mu da ƙoƙarin mu, basu zama ba sai akan kanmu.

﴿وَمَن جَٰهَدَ فَإِنَّمَا يُجَٰهِدُ لِنَفۡسِهِۦٓۚ إِنَّ ٱللَّهَ لَغَنِيٌّ عَنِ ٱلۡعَٰلَمِينَ ۝٦﴾ [العنكبوت: 6]

[Kuma wanda ya yi jihãdi, to, yanã yin jihãdin ne dõmin kansa. lalle Allah haƙĩƙa waɗatacce ne daga barin tãlikai} {6}. [Surat Al-Ankabut : 6]

Mu muna sanin cewa akwai hikima ga Allah a cikin dukkanin halittar Sa, koda mun jahilce ta, jahiltar mara lafiya da hikimar likita, baya nufin cewa rahotannin likita wasani ne.

Sanin hikimar Ubangiji, baya lazimtar masa fahimtar kowane mafi nisan hikimar , kaɗai fahimtar sashinta ya isa!

To ya isa musan cewa, mu ababen ɗorawa bautar Allah ne, kuma musan samuwar hikimar Ubangiji, to wannan yana ishe mu a ɗunkule, inba haka bafa zamu zama kamar wanda yake kafirta da dukkanin abinda baya fahimtar sa

﴿بَلۡ كَذَّبُواْ بِمَا لَمۡ يُحِيطُواْ بِعِلۡمِهِۦ وَلَمَّا يَأۡتِهِمۡ تَأۡوِيلُهُۥۚ كَذَٰلِكَ كَذَّبَ ٱلَّذِينَ مِن قَبۡلِهِمۡۖ فَٱنظُرۡ كَيۡفَ كَانَ عَٰقِبَةُ ٱلظَّٰلِمِينَ ۝٣٩﴾ [يونس: 39]

15 Sahihu Muslim, V. 7, P 257.

{A'a sun ƙaryata game da abinda ba su kewaye da saninsa ba, kuma fassararsa bata riga ta je musu ba} {39} Surat Yunus.

Allah Gwani ne, kuma Ya halicce mu dan hikima - tsarki ya tabbatar maSa -.

Allah shi kaɗai shine wanda Yake cancantar a bauta maSa.

Ba wanda ya cancanci bautawa sai Allah, shine Mahalicci wanda Ya samar da mu daga rashi - tsarki ya tabbatar maSa - Ya ce:

﴿يَـٰٓأَيُّهَا ٱلنَّاسُ ٱعۡبُدُواْ رَبَّكُمُ ٱلَّذِي خَلَقَكُمۡ وَٱلَّذِينَ مِن قَبۡلِكُمۡ لَعَلَّكُمۡ تَتَّقُونَ ٢١﴾ [البقرة: 21]

Yã ku mutãne ! Ku bauta wa Ubangjinku, Wanda Ya halicce ku, kũ da waɗanda suke daga gabãninku, tsammãninku ku kãre kanku !} (21) [Surat Al-baƙara : 21].

Shine wanda Ya shiryar damu, kuma shine Ya shara'anta ya kuma ƙaddara Yayi umarni Yayi hani.

Al-láh no sólo es el Creador, sino que es también Quien dictamina las órdenes y que debemos obedecerle -Glorificado sea-.

﴿إِنَّ رَبَّكُمُ ٱللَّهُ ٱلَّذِي خَلَقَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضَ فِي سِتَّةِ أَيَّامٖ ثُمَّ ٱسۡتَوَىٰ عَلَى ٱلۡعَرۡشِۖ يُغۡشِي ٱلَّيۡلَ ٱلنَّهَارَ يَطۡلُبُهُۥ حَثِيثٗا وَٱلشَّمۡسَ وَٱلۡقَمَرَ وَٱلنُّجُومَ مُسَخَّرَٰتِۢ بِأَمۡرِهِۦٓۗ أَلَا لَهُ ٱلۡخَلۡقُ وَٱلۡأَمۡرُۗ تَبَارَكَ ٱللَّهُ رَبُّ ٱلۡعَٰلَمِينَ ٥٤﴾ [الأعراف: 54]

{Ku saurara, halitta da umarni na sane} {54}. [Surat Al-A'araf : 54].

Allah bawai halitta ne kawai gareshi ba, kaɗai umarni ya tabbata gareshi, mu muna umartuwa da umarnin sa - tsarki ya tabbatar maSa -.

Ibada itace haƙƙin Allah akan bayinSa, domin cewa shi - tsarki ya tabbatar masa - shine wanda Ya halicce mu Yaraya mu, Ya azirta mu Ya shiryar damu, Ya aiko mana da Manzannin Sa dan Ya jarraba mu, waye acikin mu mafi kyautata aiki, to Ibada itace haƙƙin Allah akan mu.

﴿ٱلَّذِي خَلَقَ ٱلۡمَوۡتَ وَٱلۡحَيَوٰةَ لِيَبۡلُوَكُمۡ أَيُّكُمۡ أَحۡسَنُ عَمَلٗاۚ وَهُوَ ٱلۡعَزِيزُ ٱلۡغَفُورُ ٢﴾ [الملك: 2]

{Shi ne Wanda Ya halitta mutuwa da rãyuwa domin Ya jarraba ku, Ya nũna wãye daga cikinku ya fi kyãwon aiki, Shi ne Mabuwãyi, Mai gafara}.{2}. [Surat AlMulk: 2].

Kuma rayuwarmu bazata daidaita ba da ƙarshen mu sai da ibada, kuma ɗabi'unmu baza su gyaruba sai da ita, ibada tana hani abisa munanan ayyuka da ababen ƙi, kuma duniyar mutane tana gyaruwa da ita Ubangijin mu - maɗaukakin sarki - Ya ce:

﴿ٱتۡلُ مَآ أُوحِيَ إِلَيۡكَ مِنَ ٱلۡكِتَٰبِ وَأَقِمِ ٱلصَّلَوٰةَۖ إِنَّ ٱلصَّلَوٰةَ تَنۡهَىٰ عَنِ ٱلۡفَحۡشَآءِ وَٱلۡمُنكَرِۗ وَلَذِكۡرُ ٱللَّهِ أَكۡبَرُۗ وَٱللَّهُ يَعۡلَمُ مَا تَصۡنَعُونَ ٤٥﴾ [العنكبوت: 45]

{Ka tsaida sallah lallai sallah tana hani daga alfasha da munkari} {45}. [Surat Al-Ankabut: 45]

Baza mu rabauta da Aljanna ba, sai da ibada, itace tsira a lahira da farin ciki a duniya.

Ibada gare mu ta tabbata garemu da kuma alherinmu mu, ita wajibace akan mu a ɓangaren Allah - mai girma da ɗaukaka -؛ domin cewa shine Mahaliccin mu, kuma amfaninta yana komawa agare mu, mu kawai, kuma taƙaitawa acikinta yana komawa akanmu mu kawai.

Aljanna mai tsada ce, duk wanda yake san Aljanna to yayi aiki sabo da ita, mu masu buƙatuwa ne zuwa gare Shi - tsarki ya tabbatar maSa -... masu buƙatuwa ne da bautar Sa, Shine Mawadaci gare mu da kuma dukkanin halittar Sa.

21- Ta yaya zamu san Allah?

Amsa: Muna sanin Allah ta hanyoyi da yawa sosai, sai dai za mu ambaci hanyoyi huɗu a nan:

Hanya ta farko: Muna sanin Allah ta hanyar kuɓutacciyar ɗabi'ar da aka halicci mutum akan ta.

Mutum da ɗabi'ar sa da aka halicceshi akan ta, yana sanin cewa lallai akwai wani mahalicci gare shi, kai ta hanyar ɗabi'ar da aka halicceka akanta kake sanin cewa lallai kana da wani mahaliccin da Ya halicce ka, da wannan kama, da waɗanan gaɓɓan, da wannan halittar, da wannan aikin da kyautatawar mai ɗimautarwa.

Kuma mutum ta hanyar ɗabi'ar sa da aka halicce shi akanta, yake sanin cewa shi abin nema ne da fakewa zuwa ga Mahaliccin sa da ibada, kuma yake sani da ɗabi'ar sa wacce aka halicce shi akanta cewa shi mai buƙatuwane ga Mahaliccin Sa - tsarki ya tabatar masa - kuma Mai

buƙatuwa ne zuwa gare Shi a cikin kowane lokaci, wannan jin yana ƙaruwa ne da buƙatawa zuwa ga Allah acikin tsanance-tsanance.

To ɗabi'ar sanin Allah itace aka ɗabi'anci kowane mutum akanta, Alah - maɗaukakin sarki - Ya ce:

﴿فَأَقِمْ وَجْهَكَ لِلدِّينِ حَنِيفًا ۚ فِطْرَتَ ٱللَّهِ ٱلَّتِي فَطَرَ ٱلنَّاسَ عَلَيْهَا ۚ لَا تَبْدِيلَ لِخَلْقِ ٱللَّهِ ۚ ذَٰلِكَ ٱلدِّينُ ٱلْقَيِّمُ وَلَٰكِنَّ أَكْثَرَ ٱلنَّاسِ لَا يَعْلَمُونَ ٣٠﴾ [الروم: 30]

{Sabõda haka, ka tsayar da fuskarka ga addini, kanã mai karkata zuwa ga gaskiya, halittar Allah da Ya halitta mutãne a kanta. Bãbu musanyãwa ga halittar Allah, wannan shĩ ne addini madaidaici kuma amma mafi yawan mutãne ba su sani ba} {30}. [Surat Al-Rum : 30].

Kuma tsarki ya tabbatar maSa Ya ce :

﴿وَإِذْ أَخَذَ رَبُّكَ مِنۢ بَنِىٓ ءَادَمَ مِن ظُهُورِهِمْ ذُرِّيَّتَهُمْ وَأَشْهَدَهُمْ عَلَىٰٓ أَنفُسِهِمْ أَلَسْتُ بِرَبِّكُمْ ۖ قَالُوا۟ بَلَىٰ ۛ شَهِدْنَآ ۛ أَن تَقُولُوا۟ يَوْمَ ٱلْقِيَٰمَةِ إِنَّا كُنَّا عَنْ هَٰذَا غَٰفِلِينَ ١٧٢﴾ [الأعراف: 172]

{Kuma a lõkacin da Ubangijinka Ya karɓi (alkawari) daga ɗiyan Ãdam, daga bãyayyakinsu, a zuriyarsu, kuma Ya shaidar da su a kan rãyukansu, (Ya ce): "Shin, bã Nĩ ne Ubangijinku ba?" Suka ce: "Na'am! Mun yi shaida!" (ya ce): "Kada ku ce a Rãnar Kiyãma: Lalle ne mũ, daga wannan, gafalallu ne}.{172} [Surat Al-A'araf: 172].

Kafin a halicce mu, an ɗabi'antar damu akan sanin Allah, kuma an ɗabi'antar da mu akan bauta gare Shi - tsarki ya tabbatar maSa -. {Kuma ya shaidar musu akan rayukan su (Yace) Shin banine Ubangijin ku ba? sukace: Na'am, mun shaida}. Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi - ya faɗa acikin hadisi da aka haɗu akan ingancin sa: Babu wani abin haifa sai ana haifar sa ne akan ɗabi'a. .[16]

Dukkanin mu ana haifar mu akan wannan ɗabi'ar, wannan ɗabi'ar tana isar kowane mutumin da yake nufin gaskiya da ya kafa hujja akan gaskiya, kuma ya miƙa wuya ga wannan gaskiyar duk lokacin data bayyana gareshi.

Wannan ɗabi'ar, babu wanda zai yi musunta har mafi tsananin mutane a kafirci, musamman ma alokutan tsanani, mutane dukkanin su suna fakewa ga Allah a cikin lokutan tsanance-tsanance, suna manta abin da suke shirka da shi.

﴿وَإِذَا مَسَّكُمُ ٱلضُّرُّ فِى ٱلْبَحْرِ ضَلَّ مَن تَدْعُونَ إِلَّآ إِيَّاهُ ۖ فَلَمَّا نَجَّىٰكُمْ إِلَى ٱلْبَرِّ أَعْرَضْتُمْ ۚ وَكَانَ ٱلْإِنسَٰنُ كَفُورًا ٦٧﴾ [الإسراء: 67]

{Kuma idan cũta ta shãfe ku, a cikin tẽku, sai wanda kuke kira ya ɓace fãce Shi. To, a lõkacin da Ya tsira da ku zuwa, ga tudu sai kuka bijire. Kuma mutum ya kasance mai yawan butulci} {67}. [Surat Al-Isra; i: 67].

Idan mutum ya kasance a cikin baƙin ciki mai tsanani, ya kuma ji alamar halaka, to lallai cewa shi ba zai kira kowa ba sai Allah, kuma zai manta dukkanin shirkokin sa, wannan ikhlasin ga Allah acikin addu'a

16 Sahihu Muslim, H: 2658.

alokacin tsanance-tsanance abin da ya tura shi shine kuɓutacciyar ɗabi'a samammiya a cikin kowane mutum.

Daya daga shugaban nin Amurka - Eisenhower - yana cewa, kuma ya kasance jagora ne na sojojin Amurka, a yaƙin duniya na biyu yana cewa bayan ya ga yanda rundunar suke komawa da ɗabi'a a lokacin haɗari mai tsanani: " Ba'a samun mulhidai a cikin gwalalalai"[17] .

A cikin gwalalo a lokacin yaƙi, ba'a samun wani mai musun Allah, kowa yana komawa ne ga Allah, to wannan itace haƙiƙanin ɗabiar da akasa kowane mutum da ita a lokacin tsanance-tsanance.

Hanya ta biyu ga sanin Allah shine hankali: Mu muna sanin Allah ta hanyar hankali.

Allah - maɗaukakin sarki - Ya ce :

﴿أَمۡ خُلِقُواْ مِنۡ غَيۡرِ شَيۡءٍ أَمۡ هُمُ ٱلۡخَٰلِقُونَ ٣٥﴾ [الطور: 35]

{Shin, an halitta su ne bã daga kõme ba, kõ kuwa sũ ne mãsu yin halitta ?} [Surat : Al-Dur : 35].

Da hanakali anan akwai abubuwan ɗauka uku basu da na huɗu :

Na farko : Ya kasance an halicce mu ba tare da mahallici ba (Shin, an hallice su ne ba tare da komai ba) wannan korarre ne, dan ta yaya za'a halicce mu ba tare da mahallici ba ?

Na biyu : Ya zama mun halicci kawunan mu (Ko kuma sune masu yin halittar), wannan korarrene kuma, dan ta yaya zan halicci kaina kafin a halicce ni ?

17 https://en.wikipedia.org/wiki/there-are-no-athesist-in-foxholes

A wannan lokacin ta hanyar hankali abin ɗauka na uku zai rage shine wanda Ayar mai girma tayi shiru game dashi؛ domin cewa shi shine bayyananne, kuma shine lallai cewa muna da wani mahallicin da ya halicce mu.

To mu muna sanin Allah da hankali.

Hanya ta uku ga sanin Allah itace duba acikin halittun Allah:

Duba a cikin halittar Allah, yana sanya mu agaban girman Allah - mai girma da ɗaukaka –

﴿قُلِ ٱنظُرُواْ مَاذَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۚ وَمَا تُغۡنِي ٱلۡأٓيَٰتُ وَٱلنُّذُرُ عَن قَوۡمٖ لَّا يُؤۡمِنُونَ ١٠١﴾ [يونس: 101]

{Kace ku duba menene acikin sammai da kasa} {101}. [Surat Yunus : 101].

Duk lokacin da muka yi duba zuwa zirfafan halittar Allah da mamakin kyautatawa, zamu ƙara sanin Allah.

Wannan abin da muka ambace shi ne da ya rigaya a cikin dalilin samarwa da dalilin kulawa da kyutatawa.

Hanya ta huɗu ga sanin Allah itace ta hanyar Manzanni.

Wannan shine hanya mafi girma ga sanin Allah - mai girma da ɗaukaka -, shine musan Allah ta hanyar Manzannin Sa da Annabawan Sa, Manzanni sun bada labari game da Allah kuma sun bada labari daga zatin Sa - tsarki ya tabbatar maSa - ta hanyar Annabawa muka san Allah da sunayen Sa da siffofin Sa, muka san tayaya zamu bautawa Allah kuma ta yaya zamu nemi kusanci zuwa gare Shi, kuma muka san ta yaya zamu tsira a ranar hisabi daga azabar Allah, Manzanni sun kira mutane dan bautar Allah ko da wata ma'anar daban: Sun kira mutane dan komawa

ga ɗabi'ar da aka haliccesu akan ta, kuma su bautawa Allah kamar yanda yayi umarni.

Manzanni sun shiryar da mutane zuwa hanyar gaskiya da tsira.

﴿رُّسُلًا مُّبَشِّرِينَ وَمُنذِرِينَ لِئَلَّا يَكُونَ لِلنَّاسِ عَلَى ٱللَّهِ حُجَّةٌۢ بَعْدَ ٱلرُّسُلِ ۚ وَكَانَ ٱللَّهُ عَزِيزًا حَكِيمًا ﴿١٦٥﴾﴾ [النساء: 165]

{Manzanni mãsu bãyar da bushãra kuma mãsu gargaɗi dõmin kada wata hujja ta kasance ga mutãne a kan Allah bãyan Manzannin. Kuma Allah yã kasance Mabuwãyi, Mai hikima} [165}. [Surat Al-Nisai : 165]

Bayar da labarin da waɗan nan Annabawan da Manzannin suka yi, game da Allah da ƙarfafawar Allah gare su da mu'ujizoji, ba zai sanywa wani ɗaya hujja akan Allah ranar Al-ƙiyama ba.

Allah - mai girma da ɗaukaka - Ya baka ɗabi'a da zakasan mahaliccin ka da ita, kuma Ya baka hankali, kuma Ya baka duba acikin ababen halittar Sa, Ya aiko maka Manzanni, babu wata hujja data rage gareka a wurin Allah.

22- A can akwai Addinai masu yawa, to danme yasa Musulunci?

Amsa: Musulunci ba wani Addini bane daga Addinai.

Musulunci yana dacewa a aƙidar sa da aƙidun dukkan Annabawa, tsohon alƙawari.

Musulunci shine ingantawa ga matafiyar Addinain da suka canza, da dawowa ga aƙidar Annabawa tsohon alƙawari na kaɗaita Allah.

Allah - maɗaukakin sarki - Yana cewa:

﴿۞ شَرَعَ لَكُم مِّنَ ٱلدِّينِ مَا وَصَّىٰ بِهِۦ نُوحًا وَٱلَّذِىٓ أَوْحَيْنَآ إِلَيْكَ وَمَا وَصَّيْنَا بِهِۦٓ إِبْرَٰهِيمَ وَمُوسَىٰ وَعِيسَىٰٓ ۖ أَنْ أَقِيمُوا۟ ٱلدِّينَ وَلَا تَتَفَرَّقُوا۟ فِيهِ ۚ كَبُرَ عَلَى ٱلْمُشْرِكِينَ مَا تَدْعُوهُمْ إِلَيْهِ ۚ ٱللَّهُ يَجْتَبِىٓ إِلَيْهِ مَن يَشَآءُ وَيَهْدِىٓ إِلَيْهِ مَن يُنِيبُ ﴿١٣﴾﴾ [الشورى: 13]

{Ya shar'anta muku, game da addini, abin da Ya yi wasiyya da shi ga Nũhu da abin da Muka yi wahayi da shi zuwa gare ka, da abin da Muka yi wasiyya da shi ga Ibrãhĩm da Mũsã da Ĩsã, cẽwa ku tsayar da addini sõsai kuma kada ku rarrabu a cikinsa. Abin da kuke kira zuwa gare shi, ya yi nauyi a kan mãsu shirki. Allah na zãɓen wanda Yake so zuwa gare Shi, kuma Yanã shiryar da wanda ke tawakkali gare Shi, ga hanyarSa} {13}. [Surat Al-Shura: 13]

Musulunci ba Addinine kamar Addinai ba kaɗai shi asalin Addinai ne.

23- Menene Musulunci?

Amsa: Musulunci shine: Miƙa wuya da ƙanƙar da kai da jawuwa ga Allah - maɗaukakin sarki -.

Sha'anin sa ya ɗaukaka Ya ce :

﴿وَمَنْ أَحْسَنُ دِينًا مِّمَّنْ أَسْلَمَ وَجْهَهُۥ لِلَّهِ وَهُوَ مُحْسِنٌ وَٱتَّبَعَ مِلَّةَ إِبْرَٰهِيمَ حَنِيفًا ۗ وَٱتَّخَذَ ٱللَّهُ إِبْرَٰهِيمَ خَلِيلًا ﴿١٢٥﴾﴾ [النساء: 125]

{Kuma wãne ne ya fi kyau ga addini daga wanda ya sallama fuskarsa ga Allah, alhãli kuwa yanã mai kyautatawa kuma ya bi aƙidar Ibrãhĩm, Yanã mai karkata zuwa ga gaskiya? Allah Yã riƙi Ibrãhĩm badãɗayi} {125}. [Surat Al-Nisai: 125]

Ma'anar ya sallama fuskar sa ga Allah: Wato ya miƙa wuya ga Allah ya jawu gare Shi tsarki ya tabbatar maSa Ya ɗaukaka kuma Ubangijin mu Ya tsarkaka, wannan shine mafi kyan mutane a Addini.

kuma Allah - maɗaukakiN sarki - Ya ce:

﴿وَلِكُلِّ أُمَّةٍ جَعَلْنَا مَنسَكًا لِّيَذْكُرُوا۟ ٱسْمَ ٱللَّهِ عَلَىٰ مَا رَزَقَهُم مِّنۢ بَهِيمَةِ ٱلْأَنْعَٰمِ ۗ فَإِلَٰهُكُمْ إِلَٰهٌ وَٰحِدٌ فَلَهُۥٓ أَسْلِمُوا۟ ۗ وَبَشِّرِ ٱلْمُخْبِتِينَ ﴿٣٤﴾﴾ [الحج: 34]

{Ubangijinu Ubangiji ne ɗaya sai ku sallama maSa, kuma kayi bushara ga masu ƙanƙar da kai} {34} [Surat Al-Hajj : 34].

Ma'anar sai ku sallama maSa, wato : ku miƙa wuya ga hukuncin Sa.

Waɗan nan ayoyin, suna fa'idantar da cewa ma'anar Musulunci shine miƙa wuya a sake ga Allah - maɗaukakin sarki -, da jawuwa gare Shi Ya ɗaukaka acikin ɗaukakar Sa, da kamantawa ga shari'ar Sa da hanyar Sa, da yarda da karɓa, wannan shine jauharin Musulunci kuma haƙiƙar sa.

Musulunci shine miƙa wuya ga Allah a cikin hukuncin Sa da shari'ar Sa.

Musulunci shine Addinin Allah ga dukkanin mutane, Allah - maɗaukakin sarki - Ya ce :

﴿إِنَّ ٱلدِّينَ عِندَ ٱللَّهِ ٱلۡإِسۡلَٰمُۗ وَمَا ٱخۡتَلَفَ ٱلَّذِينَ أُوتُواْ ٱلۡكِتَٰبَ إِلَّا مِنۢ بَعۡدِ مَا جَآءَهُمُ ٱلۡعِلۡمُ بَغۡيَۢا بَيۡنَهُمۡۗ وَمَن يَكۡفُرۡ بِـَٔايَٰتِ ٱللَّهِ فَإِنَّ ٱللَّهَ سَرِيعُ ٱلۡحِسَابِ ١٩﴾ [آل عمران: 19]

{Lallai Addini a wurin Ubangiji (shine) Musulunci} {19} [Surat Aal-Imran: 19].

Musulunci shine Addinin da Allah baya karɓar wanin sa daga Addinai.

﴿وَمَن يَبۡتَغِ غَيۡرَ ٱلۡإِسۡلَٰمِ دِينٗا فَلَن يُقۡبَلَ مِنۡهُ وَهُوَ فِي ٱلۡأٓخِرَةِ مِنَ ٱلۡخَٰسِرِينَ ٨٥﴾ [آل عمران: 85]

{Kuma wanda ya nẽmi wanin Musulunci ya zama addini, to, bã zã a karɓa daga gare shi ba. Kuma shi a Lãhira yana daga cikin mãsu hasãra} {85}. [Surat Aal-Imran: 85].

Musulunci shine Addinin da Allah ya aiko dukkanin Annabawa da Manzanni da shi, Addinin Annabawa ɗaya ne shine Musulunci, dukkanin Annabawa sunzo da Tauhidi koda shari'un su sun saɓa.

Allah - maɗaukakin sarki - Ya ce :

﴿وَمَآ أَرۡسَلۡنَا مِن قَبۡلِكَ مِن رَّسُولٍ إِلَّا نُوحِيٓ إِلَيۡهِ أَنَّهُۥ لَآ إِلَٰهَ إِلَّآ أَنَا۠ فَٱعۡبُدُونِ ٢٥﴾ [الأنبياء: 25]

{Kuma ba Mu aiki wani Manzo ba a gabãninka fãce Munã yin wahayi zuwa gare shi, cẽwa "Lalle ne Shi, bãbu abin bautãwa fãce Nĩ, sai ku bauta Mini} {25}. [Surat Al-Anbiya: 25].

Babu wani Addini da yayi ragowa akan wannan Tauhidin sai Musulunci.

Musulunci shine Addinin Tauhidi mafi kaɗaituwa a yau a bayan ƙasa.

Yayin da dukkanin masu dangantuwa ga wasu Shari'un daban wani rabo na shirka ya wayi gari agare su ya ƙaranta ko ya yayi yawa, bayan mutuwar Annabawa, kuma bayan sun bar mutane akan Tauhidi, sai mutane suka riƙi shirkoki tare da lokaci, babu wani Addinin da ya rage a yau da yake akan tsarkakakken Tauhidin da Annabawa suka zo dashi inba Musulunci ba.

24- Shin a cikin Musulunci akwai amsa ga tambayoyin da hankula suka kiɗime a cikin amsa su. daga ina muka zo? Kuma dan me yasa mu muke a nan acikin wannan duniyar? kuma ina ne makoma?

Amsa; Musulunci ya amsa dukkanin waɗan nan tambayoyin, a cikin aya ɗaya daga Al-ƙur'ani mai girma, Ubangijin mu - tsarki ya tabbatar masa - Ya ce:

﴿وَمَالِىَ لَآ أَعۡبُدُ ٱلَّذِى فَطَرَنِى وَإِلَيۡهِ تُرۡجَعُونَ٢٢﴾ [يس: 22]

{Kuma mene ne a gare ni, bã zan bauta wa Wanda Ya ƙãga halittata ba, kuma zuwa gare Shi ake mayar da ku?}. [Surat yasin: 22].

Daga ina kazo? Allah shine wanda Ya haliceni (Ya ƙagoni).

Kuma ina ni zan tafi? Da sannu zan tafi zuwa ga Allah, dan ayi mini hisabi akan aikina (Kuma gare Shi makoma take).

Saboda me yasa nazo wannan duniyar? Dan bautar Allah, dan kuma a jarraba ni.

Dan me yasa nake bautawa Allah? Yana daga ɗabi'a in bautawa Allah, wanda Ya ƙageni, to wannan itace ɗabi'ar alaka tsakanin bawa da Ubangijin sa cewa: Bawa ya bautawa Ubangijin sa kuma Mahaliccin sa. ("Kuma mene ne a gare ni, bã zan bauta wa Wanda Ya ƙãga halittata ba, kuma zuwa gare Shi ake mayar da ku?". Aya ɗaya ta tattaro amsar, mafi muhimmancin tambayoyi ukun waɗanda mutum yake ɗimaucewa dasu.

﴿وَمَالِيَ لَآ أَعۡبُدُ ٱلَّذِي فَطَرَنِي وَإِلَيۡهِ تُرۡجَعُونَ﴾ [يس: 22]

{Kuma mene ne a gare ni, bã zan bauta wa Wanda Ya ƙãga halittata ba, kuma zuwa gare Shi ake mayar da ku?}. [Surat yasin : 22].

25- Ta yaya nasan cewa Muhammad - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - Manzo ne daga Allah ?

Amsa: Yawaitar dalilan gajiyarwa, yana fa'idantar da tawaturi na ma'ana da cikakken sakankancewa.

Aristotle masanin falsafa ne ta hanyar dukkanin ayyukan sa, ba wai da wata jumlar da ya faɗeta ba ko wani bayani na falsafa daya gudanar da shi.

Da Hippoctrates likita ne ta hanyar dukkanin taron ayyukan sa na likitanci, ba wai da wata tiyata daya yita ba.

Haka nan yawaitan dalilan gajiyarwa, waɗanda aka cirato daga Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - sun fa'idantar da tawaturi na ma'ana da cikakken sakankancewa cewa shi Annabi ne.

Idan ka duba a cikin tarihin sa - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi - ka sameshi mai gaskiya ne, haƙiƙa ya shahara da gaskiya ta hanyar tabbatarwa daga mafi tsananin ƙiyayya gare shi, ba'a taɓa jifansa da

wata ƙarya ba ko iskanci, sannan shi yana bada labari da abubuwan dake ɓoye sai su afku kamar yanda suke, kafin haka aƙidar sa da yayi kira gareta tun a farkon yini ta dace tare da aƙidar Annabwa gaba ɗaya, sannan shine wanda Annabawa suke bushara da gabatowar sa - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi - tun kafin yazo da shekaru ɗaruruwa, dukkanin wannan yana fa'idantar da tawaturi na ma'ana da sakankancewa cikakke akan ingancin manzancin sa.

Sannan menene game da mafi girman ayar da yazo da ita, itace Al-ƙur'ani mai girma ?

Al-ƙur'anin da Allah Ya ƙalubalanci ma'bota bayani da suzo da kwatankwacin sa, ko da wata sura daga gare shi, amma basu aikata ba.

Faɗin Allah - mai girma da ɗaukaka -:

﴿فَإِن لَّمْ تَفْعَلُوا۟ وَلَن تَفْعَلُوا۟ فَٱتَّقُوا۟ ٱلنَّارَ ٱلَّتِى وَقُودُهَا ٱلنَّاسُ وَٱلْحِجَارَةُ ۖ أُعِدَّتْ لِلْكَٰفِرِينَ ﴿٢٤﴾﴾ [البقرة: 24]

{Baku aikata ba baza su aikata ba (Kawo sura), to, bazaku aikata ba} {24} [Surat Al-bakara : 24].

Al-ƙur'ani mai girma bai gushe ba yana ƙalubalantar masana balagar mushrikai da ma'abota fasaha, su a dukkanin wannan sun kame daga fito na fito da shi, ababen kamewa daga kawo kwatankwacin sa.

Dr. Abdullahi Daraz - Allah Yayi masa rahama - yana cewa: " Shin Manzo - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi - baya jin tsoro da wannan ƙalubalen da ya tayar da kishin su na Adabi?

Sai su zaburo dan gasa da shi, alhali su dukkaninin su masu kiyaya ne, menene wataƙilan sa zai aikata da ace wasu jama'a, daga masana balagar

su, sun haɗa kai akan su fitar da wani zance da zai rinjaye shi, ko da acikin sashin ɓangarorin sa ne?

Sannan da ransa ya ƙawata masa cewa ya fitar da wannan hukuncin ga 'yan zamanin sa, to ta yaya zai fitar dashi ga al'ummatai masu zuwa?

Tabbas wannan kasadar ba wani mutumin da yasan darajar kansa zai gabato zuwa gareta sai shi hannayen sa acike suke da tasarrufin hukunci, da labarin sama, haka nan yayi jifa da ita a tsakanin duniya, sai ta zama itace hukunci mara canzawa, dukkanin wanda yayi futo na futo da shi ya dawo da gajiyawa mabayyani, da rashin nasara mai kunyatarwa ga shuɗewar zamaninnika". .[18]

Haƙiƙa waɗan nan mushrikan sun ga cewa, tattara rundunoni, da harhaɗa ƙabilu dan yaƙar Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi - shine mafi sauƙi daga fito na fito da Al-ƙur'ani da karɓar ƙalubale, wannan shine ƙololuwar ƙoƙarin su.

﴿وَقَالَ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ لَا تَسۡمَعُواْ لِهَٰذَا ٱلۡقُرۡءَانِ وَٱلۡغَوۡاْ فِيهِ لَعَلَّكُمۡ تَغۡلِبُونَ﴿٢٦﴾﴾ [فصلت: 26]

{Kuma waɗanda suka kafirta suka ce, "Kada ku saurãra ga wannan Alkur' ãni, kuma ku yi ta yin kuwwa a ckin (lõkacin karãtun) sa, ɗammãninku zã ku rinjaya} {26}. [Surat Al-Fussilat : 26].

Larabawa gaba ɗaya ko al'ummatan da aka cirato ƙalubale gare su, basu zo da wani abu ba da mulhidai zasu huta gare shi, wanin su kuma su rabauta da shi.

---

18 Annaba'ul Azim, Dr. Abdullahi Drazar - Allah Yayi masa rahama -, shafi na 44-45.

Al'Alusy - Allah Yayi masa rahama - yana cewa: "Babu wani daga cikin su, da ya furta zuwa yau, kuma bai bayyana wani abin siffantawa ba ko wata sifa.

Jubair ɗan Muɗ'im yace alokacin bai musulunta ba: Naji Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi - yana karanta Al-Dur a cikin (Sallar) Magriba, lokacin da ya kai wannan ayar:

﴿أَمۡ خُلِقُواْ مِنۡ غَيۡرِ شَيۡءٍ أَمۡ هُمُ ٱلۡخَٰلِقُونَ ٣٥ أَمۡ خَلَقُواْ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضَۚ بَل لَّا
يُوقِنُونَ ٣٦ أَمۡ عِندَهُمۡ خَزَآئِنُ رَبِّكَ أَمۡ هُمُ ٱلۡمُصَۜيۡطِرُونَ ٣٧﴾ [الطور: 35_37]

{Shin, an halitta su ne bã daga kõme ba, kõ kuwa sũ ne mãsu yin halitta?} (35). Shin, sun halitta sammai da ƙasa ne? Ã'a ba su dai yi ĩmãnin yaƙĩni ba.(36) Shin, taskõkin Ubangijinka, sunã a wurinsu ne? Kõ kuwa sũ ne mãsu rinjãya? (37) [surat : Al-Dur : 35_37].

Yace: Zuciyata ta kusa ta shi' .[19]

Al-ƙur'ani a cikin sa akwai sirruka masu ban mamaki da suke kaiwa zuwa zuciyar mutum.

Ka lura ta yaya matan mushrikai suka kasance suna tururuwa a gefen gidan Abubakar, yayin da yake karanta Al-ƙur'ani, saboda yawan tunkuɗuka zuwa gareshi da tasirantuwar su da shi, har hakan ya razanar da mazajen Kuraishawa. .[20]

19 Sahihul Bukhari, H: 4854.

20 Sahihul Bukhari, H: 3905.

Sabo da haka kalmar jama'un Larabawa ta haɗu, akan kada suji Al-ƙur'ani kuma kada su jiyar da iyalan su shi, wannan shine hanya ɗaya dan wanzuwa akan kafirci.

Daga abubuwan mamakin Al-ƙur'ani mai girma, kuma abubuwan mamakin sa bazasu ƙare ba, abinda Dr. Abdullahi Draz - Allah Yayi masa rahama - ya faɗa a cikin mas'alar saukar ayoyin Al-ƙur'ani acikin lokuta daban-daban, sannan Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi - yana nuni zuwa sanya wasu ayoyin a cikin wasu iyakantattun wurare tsakanin surori, da wasu ayoyin daban tsakanin wasu surorin daban, sannan kowace sura a ƙarshe ta bayyana kamar wani ginine mai zaman kansa, Allah Yayi masa rahama yana cewa: "A cikin saukar Al-ƙur'ani wasu wuraren acikin Al-ƙur'ani sun kasance suna ƙaruwa a nesa daga wasu wuraren daban, kuma suna kasancewa a sannu -sannu a tattare masu zaman kansu bayan wasu ayoyin daban sun haɗu zuwa gare su a bayan su, kuma lallai cewa sashin su sun kasance ana rabasu a nan, wasunsu kuma suna shiga tare da wasun su a can, gwargwadan umarnin Manzo - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi - wanda ya kasance yake karɓar sa da aikin sa daga Rai mai tsarki.

Idan muka ɗauki tarihan da babu takaituwa gare su a izinarmu - tarihan saukar ayoyin Al-ƙur'ani mai girma -, kuma muka lura cewa, wannan wahayin ya kasance ta fuska mai gamewa, mai ta'allaƙuwa da wasu yanayai da munasabobi keɓantattu, to lallai cewa wannan zai kiramu zuwa tambaya dan gane da lokacin da aikin tsara kowace sura ya cika, akan tsarin kaɗaituwa mai zaman kansa.

Kai kace Al-ƙur'ani ya kasance wasu yankuna ne a rarrabe ababan sawa alama daga tsohon gini, da kasance ana nufin dawo da ginin sa a cikin wani wurin daban akan ainihin kamanni da ya gabata, inba haka bafa, to ta yaya fassara wannan jerantuwar ta gaggawa na manhaja zai yiwu a lokaci ɗaya, a cikin abinda ke rataye da yawa daga surori?

Sai dai wane lamunine na tarihi, mutum zai iya tabbata akansa yayin sanya misalin wannan tsarin a daura da abubuwan da zasu faru nan gaba, da ababen neman su na shara'antawa, da warware-warware ababan neman tabbatarwar su, ballantana ma game da yanayi na harshe, wanda yake wajaba a gabatar da waɗan nan warwarewar, da dacewar su na salo, tare da wannan Surar maimakon waccan?

Shin yanzu bama fitar da sakamakon cewa cikar wannan tsarin, da tabbbatar sa akan sura abar ƙauna, yana neman shigowa daga wani Mahalicci Mai girma, wanda cikakken iko yake samuwa a gare shi, akan tsaida wannan jerin abin ginawa?"[21] .

Al-ƙur'ani mu'ujiza ce mai zaman kansa akan gaskiyar Annabcin sa - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi -.

Kuma mu'ujizojin sa - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi - waɗanda suka gudana a hannayen sa masu yawa, sun haura dubu da yawa, saninsu a kusa yake, masu ciratosu sune mafiya gaskiyar halitta kuma mafi biyayyar su.

Waɗan nan maruwaitan waɗanda suka cirato waɗan nan mu'ujizojin zuwa garemu, sun kasance basa halatta ƙarya a cikin abinda ya rikitar to ta yaya zasuyi masa ƙarya, alhali su suna sanin cewa duk wanda yayi masa ƙarya da gangan to ya tanadi masaukin sa a wuta, kamar yanda shima ya gargaɗar - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi -.

Sashin mu'ujizojin sa - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi - dubun nan sahabbai sun halarce su, kuma sashin su gommai sun ruwaito su daga gare su, to ta yaya za'a haɗu akan ƙarya a dukkanin wannan?

Misali akan mu'ijozojin sa - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi - taro mai girma daga mutane sun halarce su: Hadisin shauƙin ɗin kututturen dabino shi hadisi ne mashhuri mutawatiri yayin da Annabi -

21 Kitab Madkhal ilal ƙur'anil karim, Dr. Abdullahi Draz.

tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi - ya kasance yana Huɗuba akan kututturen, yayin da akayi masa Minbari ya hau kansa yayi huɗuba sai kututturen yayi shauƙi, kuma yayi nishi irin nishin ƙaramin yaro, bai gusheba yana nishi yana shauƙi har sai da Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi - ya tattaro shi sai yayi shiru.

Wannan hadisin waɗan nan daga sahabbai sun ruwaito shi: Anas ɗan Malik, da Jabir ɗan Abdullahi, da Abdullahi ɗan Abbas, da Abdullahi ɗan Umar, da Ubayyu ɗan Ka'ab, da Abu Sa'id, da Sahlu ɗan Sa'ad, da A'isha 'yan Abubakar, da Ummu Salama.

Shin misalin wannan adadin, daga sahabbai zasu haɗu akan ƙarya a cikin ruwaito wani labari kamar wannan?

Kai sashin mu'ijizojin sa dubun nan sahabbai sun halarce su misalin ɓuɓɓugar ruwa ta tsakanin yatsun sa maɗaukaka har sahabbai dubu da ɗari biyar sukayi alwala kuma suka sha, hadisin mutawatirine, kuma Bukhari da Muslim sun ruwaito shi.

Da yawaitar ƙanƙanin abinci dan runduna mai girma suci, wannan kuma labarai mutawatirai sunzo da shi daga sahabbai, haƙiƙa Bukhari shi kaɗai ya ambata mu'ujizar yawaitar abinci akan hannun Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi - a gurare biyar daga ingantaccen littafin sa.[22] .

Idan dalilan gaskiya sun kasance matabbatane kuma mu'Ujizoji a cike suke akan Annabcin sa - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi -, to ta yaya ga mai hankali zai ƙaryata da dukkanin wannan?

---

22 Bukhari (1217), Bukhari (2618), Bukhari (3578), Bukhari (4101), Bukhari (6452). Dukkanin su abubuwa ne da suka afku mabanbanta manisanta, wannan a cikin Bukharine shi kaɗai!

Waɗan nan wasu misalai ne daban masu sauƙi daga mu'ujizojin sa - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi -:

(Annabi) - tsira da amincin Allah su tabbata agareshi, ya bada labari a cikin wani dare daga darare da cewa wata iska mai tsanani zata taso, kuma ya hana mutane daga tashi, sai wani mutum ya tashi sai iskar ta ɗauke shi ta jefar dashi a wani guri mai nisa daga gurin sa.[23] .

Kuma Anabi - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi - ya bada labari da mutuwar Najjashi a cikin yinin da ya mutu acikin sa, kuma yayi kabbara gareshi sau huɗu .[24]

Kuma Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi - ya bada labari da shahadar Umar da Usman da Ali da Dalha da Zubair - Allah ya yarda da su - gaba ɗaya, kuma cewa su bazasu mutu akan shimfiɗar su ba kamar yanda mutane suke mutuwa.

Haƙiƙa Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi - ya hau dutse wata rana shi da Abubakar da Umar da Usman da Ali da Dalha da Zubair, sai dutsen ya girgiza, sai Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi - ya cewa dutsen: "Ka nutsu, ba wanda ke kanka sai Annabi, ko Siddiƙ ko shahid". .[25]

Sai ya yiwa kansa hukunci da Annabci, ga Abubakar da gaskiya, ga ragowar kuma da cewa zasu zama shahidai, kuma abinda ya bada labari dashi ya faru.

23 Sahihu Muslim, H: 3319.

24 Sahihul Bukhari, H: 1333.

25 Sahihu Muslim, H: 2417.

Acan akwai hadisai 150 Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi - ya roƙi Ubangijin sa kuma aka amsa masa a nan take, alhali mutane suna gani! .[26]

Yayin da mutanen Makka suka tambayi Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi - daya nuna musu wata aya, sai ya nuna musu wata ya tsage gida biyu, har sukaga Hira a tsakanin su, wannan hadisin mutawatiri ne, wato shi yana cikin mafi ƙololuwar darajojin inganci.

Haƙiƙa Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi - ya kasance yana karanta Surat Al-Kamar wacce acikinta akwai mu'ujizar tsagewar wata a manyan guraren taruwa kamar Jumu'o'i da iduka dan ya jiyar da mutane abin da ke cikinta daga mu'ujizojin sa - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi -, ya kasance yana kafa hujja da ita akan gaskiyar Annabcin sa.

Sannan bada labarin Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi - da cewa Adam shine ƙarshen halitta daga kasantattu rayayyu: "Kuma ya halicci Adam bayan La'asar daga ranar Juma'a a ƙarshen halitta". .[27]

Wannan haƙiƙar ta ilimi ta zama a yanzu tabbatacciya, to ta yaya - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi - yasan cewa Adam - aminci ya tabbata a gare shi - shine ƙarshen kasantattu bayyana akan ƙasa, bayan bayyanar tsirrai da dabbobi ?

Kayi duba ga faɗin Allah - maigirma da ɗaukaka -:

---

26 Sa'idu ɗan Abdulƙadir Ba Shanfar ya tattara waɗan nan hadisan, a cikin littafin sa Dala'ilun Nubuwwah, littafin yana daga fitarwar Daru Ibn Hazm.

27 Sahihul Jami'u, 8188.

﴿وَجَعَلۡنَا ٱلَّيۡلَ وَٱلنَّهَارَ ءَايَتَيۡنِۖ فَمَحَوۡنَآ ءَايَةَ ٱلَّيۡلِ وَجَعَلۡنَآ ءَايَةَ ٱلنَّهَارِ مُبۡصِرَةٗ لِّتَبۡتَغُواْ فَضۡلٗا مِّن رَّبِّكُمۡ وَلِتَعۡلَمُواْ عَدَدَ ٱلسِّنِينَ وَٱلۡحِسَابَۚ وَكُلَّ شَيۡءٖ فَصَّلۡنَٰهُ تَفۡصِيلٗا ١٢﴾ [الإسراء: 12]

{Mun sanya dare da yini ayoyi biyu sai muka shafe ayar dare muka sanya ayar rana mai sanyawa ayi gani} {12} [Surat Al-Isra ; i: 12].

Sai muka shafe ayar dare: Wato lallai cewa wata shine ayar dare ya kasance mai haske sannan aka shafe hasken sa.

Wannan a aikace shine abinda sahabbai suka fassara ayar mai girma da shi, haƙiƙa Imam Ibn Kasir ya ruwaito a cikin tafsirin sa cewa Abdullahi ɗan Abbas - Allah Ya yarda dasu - yace: "Wata ya kasance yana haske kamar yanda rana take haske, shine ayar dare, sai aka shafe".

Abin mamaki cewa wannan shine abinda ilimi ya tiƙe gare shi a yau, hakika NASA ta yaɗa akan shafinta na hukumance da tasharta ta hukumance: Lokacin sa na farko daga rayuwar wata acikinta ya kasance mai haske ne mai kunnuwar haske. [28]

Haƙiƙa ya tabbata a tawaturi afkuwar ayoyi da bada labari da abubuwan da ke ɓoye da zirfafan sirrikan ƙasa da sammai waɗanda bubu taƙaituwa garesu akan hannun mutum ɗaya - tsira da amincin Allah su tabbata agareshi - da saukar Al-ƙur'ani agareshi, kuma yazo da abinda Annabawan dake kafinsa suke akansa, ya kasance abin ƙarfafawa daga wurin Allah bai mutu ba har saida shari'a ta cika ta kammala.

To ka yanke magana da cewa shi Annabine shine mai yawan shiryar da hankali.

---

28 http:/www.nasa.gov/mission/LRO/news/vid-tour.html

https://www.youtube.com/watch?v=UIKmSQqp8wY

Ayoyin sa - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi - na ɓoye sun haura dubu.

Masu cirato mu'ujizoji sune sahabban sa mafi gaskiyar halitta kuma mafi biyayyar su a bayan sa.

Abin mamaki cewa manyan sahabbai sun musulunta kafin suga mu'ujizoji, su sun musulunta domin cewa su suna sanin cewa Annabi Muhammad - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi - mai gaskiya ne, kuma cewa shi bai taɓa ƙarya ba ko sau ɗaya tun da yake.

Wannan matsayar daga manyan sahabbai, shine matsayar hankali mai hikima, gaskiyar Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi - daliline isashshe mai zaman kansa dan tabbatar da ingancin Annabta... wannan domin cewa mutumin da yake da'awar Annabta, ko dai ya zama: Mafi gaskiyar mutane, domin cewa shi Annabi ne... Annabi shine mafi gaskiyar mutane.

Ko ya zama: Mafi ƙaryar mutane, domin cewa shi yana ƙirƙirar ƙarya a cikin mafi giraman al'amura a sha'ani.

Kuma mafi gaskiyar mutane baya cakuɗuwa da mafi ƙaryar mutane, sai ga mafi jahilcin mutane. [29]

Ya mamakin mafi sauƙin mai hankali ya sami ikon banbance tsakaknin mafi gaskiyar mutane da mafi ƙaryar mutane.

Haƙiƙa mushrikai sunyi furuci a farkon yini daga aiko shi - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi - cewa shi bai taɓa ƙarya ba ko sau ɗaya, sai suka ce da shi: "Bamu taɓa jarraba ƙarya gare ka ba".

29 Subutun Nubuwwat Aƙlan wa Naƙlan, Ibn Taimiyya, Dar Ibn Jauzi, shafi 573, da ma'anarsa a cikin ainihin littafin shafi 318.

Yayin Hiraƙl ya tambayi Abu Sufyan, kafin ya musulunta: "Shin kun kasance kuna zagin sa da ƙarya kafin ya faɗi abinda ya faɗa?".

Sai Abu Sufayn yace: "A'a".

Sai Hiraƙl yace: "Bazai kasance zai bar yin ƙarya ga mutane ba kuma yayiwa Allah ƙarya".

Sannan Hiraƙl ya kammala, sai ya faɗi maganar sa mashahuriya: "Da na kasance a wurin sa, da na kasance na wanke diga-digan sa".

Haƙiƙa kafirai sun gajiya, daga bayyanar da wata ƙarya ɗaya a cikin rayuwar sa - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi -, saboda haka Al-ƙur'ani yayi musun kafirci akan su tare da sanin su da halin sa kafin aiko shi sai Ubangijin mu - tsarki Ya tabbatar ma Sa - Ya ce :

﴿أَمۡ لَمۡ يَعۡرِفُواْ رَسُولَهُمۡ فَهُمۡ لَهُۥ مُنكِرُونَ٦٩﴾ [المؤمنون: 69]

{Kõ ba su san Manzonsu ba ne dõmin haka suke mãsu musu a gare shi?} {69} [Surat Al-Muminun: 69].

Halin Annabi da tarihin sa, dalili ne mai zaman kansa akan cewa shi Annabi ne.

Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi.

Idan dalilan gaskiya sun kasance masu gamewane masu ƙarfafawa akan Annabcin sa - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi -, to ta yaya ga mai hankali zai ƙaryata da dukkanin wannan?

26- Ta yaya zansan cewa ni abin nema ne da imani da Allah?

Amsa; Kayi duba ga kanka, zakasan cewa, kai abin jarrabawane, shin bai zamo a cikinka akwai ji ba, ka aikata dadai kada ka aikata kuskure?

Da ace a gaban ka akwai wasu dukiyoyi, kuma ma'abocin su ya shagalta daga gare su, to cewa wani ji zaizo maka, ka kaɗauki waɗan nan dukiyoyin kayi amfani dasu, da wani jin mai fuskantarwa yana ce maka: Kada ka aikata hakan to wannan haramun ne kuma laifine.

Kai abin jarrabawa ne acikin kowacce matsaya daga rayuwarka.

Wannan jin - jin ka aikata kada ka aikata - ana samu a cikin ka, domin cewa kai a aikace abin jarrabawane, baka zama abin bari ba... baka zama komai ba ba tare da ƙima ba.

Allah - Maɗaukakin sarki - Ya ce :

﴿إِنَّا هَدَيْنَٰهُ ٱلسَّبِيلَ إِمَّا شَاكِرًا وَإِمَّا كَفُورًا﴿٣﴾﴾ [الإنسان: 3]

{Lalle ne, Mũ, Mun shiryar da shi ga hanyar ƙwarai, ko ya zama mai gõdiya, kuma ko ya zama mai kãfirci} {3}. [Surat Al-Insan: 3].

Mutum a cikinsa akwai ka aikata kar ka aikata: To shi ko dai mai godewa ne ko mai butulcewa ne a kowane matsaya daga rayuwar sa.

Kai a kowane mataki daga matakan rayuwar mutum, zai yiwu ga mutum da ya aikata alheri ko ya aikata sharri, shin yana tafiya dan masallaci ne ko kuma yana tafiya ne dan wasa.

Sabo da haka Allah - maigirma da ɗaukaka - Ya ce :

﴿وَمَا خَلَقْتُ ٱلْجِنَّ وَٱلْإِنسَ إِلَّا لِيَعْبُدُونِ﴿٥٦﴾﴾ [الذاريات: 56]

{Kuma Ban halitta aljannu da mutãne ba sai dõmin su bauta Mini} {56}. [Surat Al-Zariyat : 56].

A cikin kowane mataki, zaka sami wani nau'i daga bauta ga Allah ko saɓa maSa - tsarki ya tabbatar maSa -.

Wanda aka datar ga aikata abinda Allah Ya umarce shi da shi ya tsira, wanda ya saɓawa abinda Allah Ya umarce shi da shi yayi kuskure.

Wannan zaɓi, hisabin mutum yana tabbatuwa akan sa, abisa dukkan abinda ya aikata .

Manufar halittar mu a jarraba mu, wannan itace manufar da Allah Ya aiko Manzanni sabo da ita, kuma ya saukar da littattafai.

﴿وَلَقَدۡ بَعَثۡنَا فِي كُلِّ أُمَّةٖ رَّسُولًا أَنِ ٱعۡبُدُواْ ٱللَّهَ وَٱجۡتَنِبُواْ ٱلطَّٰغُوتَۖ فَمِنۡهُم مَّنۡ هَدَى ٱللَّهُ وَمِنۡهُم مَّنۡ حَقَّتۡ عَلَيۡهِ ٱلضَّلَٰلَةُۚ فَسِيرُواْ فِي ٱلۡأَرۡضِ فَٱنظُرُواْ كَيۡفَ كَانَ عَٰقِبَةُ ٱلۡمُكَذِّبِينَ٣٦﴾ [النحل: 36]

{Tabbas mun aiko cikin kowace al'umma wani manzo da ya isar da saƙon ku bautawa Allah kuma ku nesanci dagutu (duk wani abin bauta da ba Allah ba)} {36}. [Surat Al-Nahl: 36].

Bayan jarrabawa ta ƙare da mutuwa, zamu koma zuwa ga Allah

﴿وَمَا لِيَ لَآ أَعۡبُدُ ٱلَّذِي فَطَرَنِي وَإِلَيۡهِ تُرۡجَعُونَ٢٢﴾ [يس: 22]

{Kuma gare Shi ne za'a mai da ku} {22} Surat Yasin.

﴿وَأَنَّ إِلَىٰ رَبِّكَ ٱلۡمُنتَهَىٰ ٤٢﴾ [النجم: 42]

{Kuma lallai zuwa ga Ubangijinka Matuƙa ta ke} {42}. [Surat Al-Najm : 42].

﴿إِنَّ إِلَىٰ رَبِّكَ ٱلرُّجۡعَىٰٓ ﴿٨﴾﴾ [العلق: 8]

{Lallai ne makoma ga Ubangijinka take} {8}. [Surat Al-Alaƙ : 8]

Surah Al Alaq (La célula embrionaria)

Mu zamu koma zuwa Allah, dan ayi mana hisabi akan abin da muka gabatar.

﴿ثُمَّ يُجۡزَىٰهُ ٱلۡجَزَآءَ ٱلۡأَوۡفَىٰ ﴿٤١﴾﴾ [النجم: 41]

{Kuma lallai za'aga Ayyukan sa} {40} {Sannan sai a saka masa da cikakken sakamako} {41}. [Surat Al-Najm: 41].

Da sannu za'aga abin da ka gabatar daga aiki kuma ayi maka hisabi akan hakan

﴿فَمَن يَعۡمَلۡ مِثۡقَالَ ذَرَّةٍ خَيۡرٗا يَرَهُۥ ﴿٧﴾ وَمَن يَعۡمَلۡ مِثۡقَالَ ذَرَّةٖ شَرّٗا يَرَهُۥ ﴿٨﴾﴾ [الزلزلة: 7-8]

{To, wanda ya aikata (wani aiki) gwargwadon nauyin zarra, na alheri, zai gan shi} {7}. {Kuma wanda ya aikata gwargwadon nauyin zarra na sharri, zai gan shi} {8}. [Surat Al-Zilzala: 7-8].

27- Shin imani da Allah ya isa da kafircewa da Annabawa?

Amsa: A'a.

Imani da samuwar Allah tare da rashin yin imani da Annabawa baya isuwa, har sai mutum ya kasance mai miƙa wuya ga Allah, to meye ma'anar kayi imani da cewa Allah shine Mahalicci Mai azirtawa Mai

jujjuya al'amura, sannan ka kafirce da wahayinsa kayi musun Manzannin sa?

Wannan shine kafirci mafi girma.

Kai a can babu wani abu mafi girman laifi daga wanda yake dawowa da Allah wahayin Sa, Allah - maɗaukain sarki - Ya ce:

﴿إِنَّ ٱلَّذِينَ يَكۡفُرُونَ بِٱللَّهِ وَرُسُلِهِۦ وَيُرِيدُونَ أَن يُفَرِّقُواْ بَيۡنَ ٱللَّهِ وَرُسُلِهِۦ وَيَقُولُونَ نُؤۡمِنُ بِبَعۡضٖ وَنَكۡفُرُ بِبَعۡضٖ وَيُرِيدُونَ أَن يَتَّخِذُواْ بَيۡنَ ذَٰلِكَ سَبِيلًا ١٥٠ أُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡكَٰفِرُونَ حَقّٗاۚ وَأَعۡتَدۡنَا لِلۡكَٰفِرِينَ عَذَابٗا مُّهِينٗا ١٥١﴾ [النساء: 150-151]

{Lalle ne, waɗanda uke kãfirta da Allah da ManzonSa kuma sunã nufin su rarrabe a tsakãnin Allah da manzanninSa, kuma sunã cẽwa: "Munã ĩmãni da sãshe, kuma munã kãfirta da sãshe." Kuma sunã nufin su riƙi hanya a tsakãnin hakan} {150}. {Waɗannan sũ ne kãfirai sõsai, kuma Mun yi tattali, dõmin kãfirai, azãba mai walãkantarwa} {151}. [Surat Al-Nisai: 151].

Wnad yayi imani da Allah, kuma ya kafirce da Annabwa, to shi kafiri ne a haƙiƙance.

Duk wanda ya kafirce da wani Annabi daga Annabawa, to shi ya kafircewa Allah, domin cewa shi yayi musun wahayin Allah, saboda haka ma'abota littafi, sun kafirta dan kafircin su da Annabcin Muhammad ɗan Abdullahi - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi.

﴿إِنَّ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ مِنۡ أَهۡلِ ٱلۡكِتَٰبِ وَٱلۡمُشۡرِكِينَ فِي نَارِ جَهَنَّمَ خَٰلِدِينَ فِيهَآۚ أُوْلَٰٓئِكَ هُمۡ شَرُّ ٱلۡبَرِيَّةِ٦﴾ [البينة: 6]

{Lalle ne waɗanda suka kafirta daga mutanen Littafi da mushirikai suna cikin wutar Jahannama suna madawwama a cikinta. Waɗannan su ne mafi ashararancin tãlikai} {6}. [Surat Al-Bayyinah: 6].

Narkon Allah da shigar su wuta gaskiya ne:

﴿وَرَبَطۡنَا عَلَىٰ قُلُوبِهِمۡ إِذۡ قَامُواْ فَقَالُواْ رَبُّنَا رَبُّ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِ لَن نَّدۡعُوَاْ مِن دُونِهِۦٓ إِلَٰهٗاۖ لَّقَدۡ قُلۡنَآ إِذٗا شَطَطًا ١٤﴾ [الكهف: 14]

{Sai narko ya tabbata} {14} Surat Kaaf.

Musulunci bai zama ba, kuma tsira bai zama ba dan kawai tabbatarwar mutum da cewa Allah shine Mahalicci Mai azirtawa, Mai rayawa, Mai kashewa, kai babu makawa daga imani da Manzannin Sa.

A wannan yayin yin imani da samuwar Allah, da kafircewa da Annabawa, baya isuwa baya amfanar da bawa a wurin Allah ranar Al-ƙiyama, dan babu makawa a bautawa Allah, kuma imani yana cika da dukkanin Manzannin Sa.

Da ace imani da samuwar Allah ya isa, da Allah bai aiko Manzannin Sa ba, kuma da bai saukar da littattafan Sa ba, domin cewa mutane gaba ɗaya suna sanin Allah ta hanyar ɗabi'ar da aka haliccesu da ita.

Allah wanda Ya halicceka Ya shiryar da kai Ya azirta ka shine Shi kaɗai Ya cancanta da ka bauta maSa kamar yanda Ya shara'anta ta hanyar Manzannin Sa da Annabawan Sa.

28- Shin kafiri zai sami lada daga Allah akan ayyukan sa na gari?

Amsa: Aiki na gari ɗabi'ane da Allah Ya ɗabi'antar da mutane akan sa, saboda haka kake ganin kowane mutum zai yiwu ya aikata wani aiki na gari koda kafiri ne ko mushriki, kowanne suna aikata ayyuka na gari da ɗabi'ar da Allah Ya ɗabi'antar dasu akan ta.

Sai dai sharaɗin karbar aiki na gari shine: A nufi zatin Allah dashi, wato: A nufi samun ladan Allah da shi.

Saboda haka mutumin da ya kafirce da Allah, wanda yake bautawa wasu Allolin daban tare da Allah, zamuce masa: Ka tafi ga waɗanda katarayyanya su tare da Allah a cikin aikin ka na gari ka samo ladanka daga gare su, kai bakayi kwaɗayin zatin Allah Shi kaɗai ba da ayyukan ka.

Ka riya wani mutumin da iyalan sa suka tsaya akan tarbiyyar sa da ciyarwa a gare shi har ya zama saurayi ƙaƙƙarfa, sannan ya tafi ga wasun su dan ya yi musu hidima, shin ya cancanta gare shi ya koma ga iyalan sa dan yace dasu: Ku bani ladan hidimar da nayiwa wasun ku?

To sai ya tafi ga waɗanda yakewa hidima ya samo ladan sa daga gare su.

Misali mafi ɗaukaka ya tabbata ga Allah.

Allah Shine wanda Ya halicce ka Ya azirta ka Yayi maka baiwa da dukkanin ni'imomi, sannan kabar bautar Sa, kuma kana son ka karɓi ladan aikin ka? yaya wannan?

Sabo da haka Allah - mai girma da ɗaukaka - Ya ce:

﴿إِنَّ ٱلَّذِينَ يَرۡمُونَ ٱلۡمُحۡصَنَٰتِ ٱلۡغَٰفِلَٰتِ ٱلۡمُؤۡمِنَٰتِ لُعِنُواْ فِي ٱلدُّنۡيَا وَٱلۡأٓخِرَةِ وَلَهُمۡ عَذَابٌ عَظِيمٞ ٢٣﴾ [النور: 23]

{Waɗanda suka kafirta ayyukan su kamar kawalwalneniya ne a faƙo mai jin ƙishirwa yana zatan cewa ruwa ne har idan yazo bai sameshi komai ba} {39}. [Surat Al-Nur : 39].

Kuma tsarki ya tabbatar maSa Ya ce

﴿وَقَدِمۡنَآ إِلَىٰ مَا عَمِلُواْ مِنۡ عَمَلٖ فَجَعَلۡنَٰهُ هَبَآءٗ مَّنثُورًا ٢٣﴾ [الفرقان: 23]

{Kuma Muka gabãta zuwa ga abin da suka aikata daga aiki, sai Muka sanya shi ƙũra wãtsattsiya} {23}. [Surat Al-Furƙan : 23]

Waɗanda suka kafirta basa cancantar sakamako akan aikin su koda na garine, domin cewa su kafiraine basuyi nufin su sami ladan Ubangijin su ba ga aiki na gari, kuma basu nemi yardar Mahaliccin su da shi ba.

Mas'alar bata zama a cikin kawai aiki na gari bane mu baki ɗaya ababen ɗabi'antarwa ne akan da yawa daga ayyuka na gari, mas'alar kawai dan me yasa ka ke aikata wannan aikin na gari, kuma wa kake aikatawa shi? shin kana aikatashi ne dan maslahar ka taka ko kana aikata shi ne dan riya, ko kana aikata shi ne ga wanin Allah?

Dukkanin wannan, ba sabo da Allah bane, kuma ba'a kwaɗayin ladan aiki na gari daga gare Shi wanda ake kwaɗayi daga Allah. 29- Idan Mususlunci shine Addinin gaskiya, to me yasa ake samun shubha (abubuwa masu rikitarwa?)

Amsa: Shubha ita wata mas'ala ce wacce musulmi baya fahimtar ta a cikin Addinin sa, haƙiƙa ta kan rikita gare shi har zuwa ya sami martani gareta.

Haƙiƙa Alah ya so - tsarki ya tabbatar maSa - da ya kasance a can akwai wasu al'amura masu rikitarwa a cikin wasu mas'aloli na rassa daga Addini, har wanda yake nufin ɓarna daga biyayya ga Ubangijin sa ya nisanta da su.

Allah - mai girma da ɗaukaka - Ya ce:

﴿هُوَ ٱلَّذِيٓ أَنزَلَ عَلَيۡكَ ٱلۡكِتَٰبَ مِنۡهُ ءَايَٰتٞ مُّحۡكَمَٰتٌ هُنَّ أُمُّ ٱلۡكِتَٰبِ وَأُخَرُ مُتَشَٰبِهَٰتٞۖ فَأَمَّا ٱلَّذِينَ فِي قُلُوبِهِمۡ زَيۡغٞ فَيَتَّبِعُونَ مَا تَشَٰبَهَ مِنۡهُ ٱبۡتِغَآءَ ٱلۡفِتۡنَةِ وَٱبۡتِغَآءَ تَأۡوِيلِهِۦۖ وَمَا يَعۡلَمُ تَأۡوِيلَهُۥٓ إِلَّا ٱللَّهُۗ وَٱلرَّٰسِخُونَ فِي ٱلۡعِلۡمِ يَقُولُونَ ءَامَنَّا بِهِۦ كُلّٞ مِّنۡ عِندِ رَبِّنَاۗ وَمَا يَذَّكَّرُ إِلَّآ أُوْلُواْ ٱلۡأَلۡبَٰبِ ٧﴾ [آل عمران: 7]

{Shi ne wanda ya saukar da Littãfi a gare ka, daga cikinsa akwai ãyõyi bayyanannu, su ne mafi yawan Littãfin, da wasu mãsu kamã da jũna. To, amma waɗanda yake a cikin zukãtansu akwai karkata sai suna bin abin da yake da kamã da jũna daga gare shi, dõmin nẽman yin fitina da tãwĩlinsa. Kuma bãbu wanda ya san tãwĩlinsafãce Allah. Kuma matabbata a cikin ilmi sunã cẽwa: "Mun yi ĩmãni da Shi; dukkansa daga wurin Ubangijinmu yake." Kuma bãbu mai tunãni fãce ma'abũta hankula} [7]. [Surat Aal-Imran: 7].

Amma waɗanda a cikin zukatan su akwai karkata sai suna bin abin da yake da kama da juna daga gare shi: Wanda acikin zuciyar sa akwai

karkata zai bi waɗan nan shubuhohin dan neman fitina da neman nisanta daga Allah.

Haƙiƙa Allah Ya so da hikimar Sa da ya kasance acan akwai imani da kafirci.

﴿هُوَ ٱلَّذِى خَلَقَكُمْ فَمِنكُمْ كَافِرٌ وَمِنكُم مُّؤْمِنٌ ۚ وَٱللَّهُ بِمَا تَعْمَلُونَ بَصِيرٌ ۝٢﴾ [التغابن: 2]

[Daga gareku akwai kafiri kuma daga gareku akwai mumini} {2} [Surat Al-Tagabun: 2}.

Sai wanda yake son kafirci yake rataya da waɗan nan shubuhohin, kuma ya shagalta da su daga Addinin sa da kuma sallar sa da imanin sa.

Amma mumini cewa shi yana bin dalilai ababen kyautatawa matabbata, waɗanda sune (Uwar littafi) akan ingancin Addini da ingancin Manzanci, da zai sami wani abun da baya fahimtar sa, to cewa shi zai tambaya game da shi, sai dai cewa shi baya shagalta da abin da baya fahimtar sa daga Addinin sa ko game da sallar sa.

Ba mai shagaltuwa daga Addinin sa da abin da baya fahimtar sa sai wanda acikin zuciyar sa akwai cuta

﴿وَمَا جَعَلْنَآ أَصْحَٰبَ ٱلنَّارِ إِلَّا مَلَٰٓئِكَةً ۙ وَمَا جَعَلْنَا عِدَّتَهُمْ إِلَّا فِتْنَةً لِّلَّذِينَ كَفَرُوا۟ لِيَسْتَيْقِنَ ٱلَّذِينَ أُوتُوا۟ ٱلْكِتَٰبَ وَيَزْدَادَ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓا۟ إِيمَٰنًا ۙ وَلَا يَرْتَابَ ٱلَّذِينَ أُوتُوا۟ ٱلْكِتَٰبَ وَٱلْمُؤْمِنُونَ ۙ وَلِيَقُولَ ٱلَّذِينَ فِى قُلُوبِهِم مَّرَضٌ وَٱلْكَٰفِرُونَ مَاذَآ أَرَادَ ٱللَّهُ بِهَٰذَا مَثَلًا ۚ كَذَٰلِكَ يُضِلُّ ٱللَّهُ مَن يَشَآءُ وَيَهْدِى مَن يَشَآءُ ۚ وَمَا يَعْلَمُ جُنُودَ رَبِّكَ إِلَّا هُوَ ۚ وَمَا هِىَ إِلَّا ذِكْرَىٰ لِلْبَشَرِ ۝٣١﴾ [المدثر: 31]

{Dan wadanda acikin zukatan su akwai cuta su ce da kuma kafirai me Allah Yake nufi da wannan ya kasance misali, haka nan Allah Yake ɓatar da wanda Yake so kuma Yake shiryar da wanda Yake so} {31}. [Surat Al-Mudassir : 31}.

Daga hikimomin samun waɗan nan shubuhohin kuma cewa waɗan nan masu kamanceceniyar ma'abota ilimi da ma'abota basira a cikin Addinin Allah suna banbanta, sai kaga malami yana sanin amsar al'amura masu rikitarwa, yana banbanta da su daga gamagarin mutum wanda baiyi zurfi ba a cikin Addini bai kuma karanceshi ba, sai Allah Ya ɗaukaka darajojin waɗanda aka bawa ilimi.

Gaskiya itace mafi bayyana, sai dai ba makawa daga samun mai rikitarwa, domin cewa shi da shi ne tantancewa yake samuwa.

Sunnar Allah a cikin halittar Sa ɗora shari'a, kuma sunnar Sa a cikin ɗora shari'a ɓoyuwar sashin hikima, marabauci shine wanda ya kafa hujja da abin da yake sani, akan abin da ya ɓuya yayi zurfi, taɓaɓɓe wanda ya sanya abin da yake jahilta shamaki da zai haramta masa daga kafa hujja da abin da yake sani.

30- Saboda me Allah ya halicci sharri? Ko da wata ma'anar daban: Ta yaya musulmi zai mayar da "Wahalar sharri"?

Amsa: Fitinar sharri, itace a taƙaice mafi girman dalillan ilhadi a tarihance.

﴿وَمِنَ ٱلنَّاسِ مَن يَعۡبُدُ ٱللَّهَ عَلَىٰ حَرۡفٖۖ فَإِنۡ أَصَابَهُۥ خَيۡرٌ ٱطۡمَأَنَّ بِهِۦۖ وَإِنۡ أَصَابَتۡهُ فِتۡنَةٌ ٱنقَلَبَ عَلَىٰ وَجۡهِهِۦ خَسِرَ ٱلدُّنۡيَا وَٱلۡأٓخِرَةَۚ ذَٰلِكَ هُوَ ٱلۡخُسۡرَانُ ٱلۡمُبِينُ ١١﴾ [الحج: 11]

{Kuma daga mutãne akwai mai bauta wa Allah a kan wani gefe. Sa'an nan idan wani alhẽri ya sãme shi, sai ya natsu da shi, kuma idan wata fitina ta sãme shi, sai ya jũya bãya a kan fuskarsa. Yã yi hasãrar dũniya da Lãhira. Waccan ita ce hasãra bayyananna} {11}. [Surat Al-Hajj: 11].

A can akwai wanda yake kafurcewa da Allah sabo da wata fitina ko wani bala'i ko wata musibar data saukar masa.

A nan mulhidi zai iya tambaya, sai yace: Me yasa a can a kwai sharri tun daga tushe?

Amsa cikin sauƙi: Domin cewa mu ababen ɗorawa shari'a ne.

Domin cewa mu acikin duniyar jarrabawa muke.

Ubangijin mu tsarki ya tabbatar maSa Ya ce :

﴿كُلُّ نَفۡسٖ ذَآئِقَةُ ٱلۡمَوۡتِۗ وَنَبۡلُوكُم بِٱلشَّرِّ وَٱلۡخَيۡرِ فِتۡنَةٗۖ وَإِلَيۡنَا تُرۡجَعُونَ ٣٥﴾ [الأنبياء: 35]

{Kuma muna jarrabar ku da sharri da alheri domin fitina} {35}. [Surat Al-Anbiya : 35].

Alheri da sharri dan cewa kai abin kallafawa shari'a ne, taklifanci shine manufar samuwar ka.

Allah - maɗaukakin sarki Ya ce :

﴿ٱلَّذِي خَلَقَ ٱلۡمَوۡتَ وَٱلۡحَيَوٰةَ لِيَبۡلُوَكُمۡ أَيُّكُمۡ أَحۡسَنُ عَمَلٗاۚ وَهُوَ ٱلۡعَزِيزُ ٱلۡغَفُورُ ٢﴾ [الملك: 2]

{Shi ne Wanda Ya halitta mutuwa da rãyuwa domin Ya jarraba ku, Ya nũna wãye daga cikinku ya fi kyãwon aiki, Shi ne Mabuwãyi, Mai gafara}.{2}. [Surat Al-Mulk: 2].

Samuwar sharri da samuwar fitintinu da masibu, shi a kan kansa, shine mafi girman dalili a bisa ingancin mas'ala ta Addini, da kuma kuskuran ilhadi.

Da mun kasance 'ya'yan duniyar madda, da bamu game fahimta ba, ba alheri babu sharri.

Da ace kasantacce ya kasance marashin ma'ana ne, da bai kasance haƙiƙa ya bayyan garemu ba a sake, cewa shi marashin ma'ana ne[30] domin cewa mu, dan dacewa ga mahangar ilhadi, zamu tafi a cikin tilascin madda mai yankewa, kuma wasu dokoki na ɗabi'a zasu gudana akan mu, a cikin wannan fagen ba zamu game fahimtar haƙiƙanin sharri ko ma'anar kalmar sharri ba.

Shin mafi yawancin dabbobi suna riskar wani ci gaba mai wahalar sharri?

Game fahimtar sharri yana nufin cewa, mu bamu zama 'ya'yan wannan duniyar ba, kuma cewa mu gamewar mu ga fahimtar sharri, yana daga wata muƙaddimar daban banda muƙaddimar madda ta Darwin (Charles Darwin) ga samuwa.

Mu muna dangantuwa ga muƙaddima ta sama, ba wai ga a yanayin ƙawatawar ilhadin madda ta ƙasa ba, wannan shine bayani ɗaya ga kasancewar mu muna game fahimtar sharri.

30 C.S. Lewis

Tun da cewa mu ababen kallafawa shari'a ne, to yana daga ɗabi'a da ya kasance a can akwai fitintinu da bala'i, kuma yana daga ɗabi'a mu game fahimtar sharri.

Saharri da sashin raɗaɗi da iko akan aikata saɓo, shine mahukunta ta ɗabi'a da sakamako bayyanan ne ga 'yancin nufi da taklif na Ubangiji.

Samuwar sharri da bala'i da masifu da sha'awoyi, waɗan nan suna fitar da mafificin abin da ke cikin mutum na gari, da mafi munin abin da ke cikin ɓataccen mutum.

Daga abin mamakin mulhidai, yayin da suke tashi da musan samuwar mahalicci, domin cewa a can akwai sharri, cewa su suna amfani da wannan binciken:

1- Idan uba ya kasance alheri ne kuma yana san alheri ga ɗan sa, a wannan yayin me yasa yayi izini ga yiwa ɗan sa allura mai raɗaɗi, dan kariya daga ƙwayoyin cuta?

2- A can akwai raɗaɗi da ya afka akan ɗan saboda allurar?

3- A wannan lokacin uba baya nan .[31]

Shin wannan sakamako ne na hankali?

Sannan cewa shi yana daga ɗabi'a cewa, mu bama fahimtar kowane zirfafan hikima ta Ubangiji a cikin alheri da sharri.

Haƙiƙa Allah Ya yaye hikima, daga ayyukan Khadiru ga sayyadina Musa - aminci ya tabbata a gare shi - tare da cewa su ayyuka ne da ake ƙirga su a bayyane, ba ababan tsagowa ba, sai dai cewa su suna ƙunshe da alheri mai girma, kuma ƙissar Musa da Khadiru bata zo acikin Al-ƙur'ani

31 Daga littafin Usus ga'ibah, M. Ahamd Hasan, cibiyar Dala'il. A taƙaice.

ba, ta babin jeranto da labarai, sai dai daga babin lura da tabbatarwa, da taƙaituwar ran mutum, da kuma hukuncinta abin gaggautowa.

Yana daga abin mamaki a cikin mas'alar sharri cewa shi: Da badan akwai sharri ba a cikin duniya, da baka fita daga gurin da aka haife ka acikin sa ba!

Kuma da aba'a samu cigaba ba, da ba a gina birane ba ko masana'antu ko gidaje, kuma da mutane basu buƙatu zuwa wani aiki ba, kuma da mutane basuyi tinani ba akan kawar da rashin lafiya, ko warware wata matsala ko ƙirƙirar wani tinani dan jawo hutu!

Kuma da mutum bai buƙaci daya cirata daga gurin haihuwar sa tun asali ba.

Dan da babu wani sharri ko wahala ko bala'i ko gajiya ko matsaloli da zaka bincika musu warwara ba.

Kuma dan me yasa gajiya da rashin barci da tinani da aiki?

Sharri shi larura ne da babu makawa daga gareta a cikin duniya!

To ka bibbiyi al'amarin!

Ka ji tsoron Allah domin cewa kai abin ɗorawa shari'a ne.

Da yawa daga mutane bala'i yana saukar musu da sharri, sai su koma zuwa ga Allah su wayi gari daga mutanen kirki, tasrki ya tabbata ga Allah mai girma da godiyar Sa.

Dukkanin ƙaddarorin Allah a cikin su akwai hikima da alheri.

Babu makawa ga musulmi, yayi imani da dukkanin ƙaddarorin Allah, Annabi - tsira da amincin Alah su tabbata agreshi - ya ce: "Da ace kana da zinare kwatankwacin dutsen Uhud, da ka ciyar dashi a cikin tafarkin Allah, ba zai karɓeshi daga gareka ba har sai kayi imani da ƙaddara, kuma kasan cewa abin da ya same ka bai kasance zai kuskure maka ba,

kuma abinda ya kuskure maka bai kasance zai sameka ba, kuma cewa shi wanda ya mutu akan wanin wannan zai shiga wuta.

Kaddarorin Allah na alheri da sharri yarda dasu yana wajaba akan musulmi.

Dukkanin ƙaddarorin Allah alheri ne, ko da sharri ya bayyana a cikin sashin su, ko ƙunci ko cuta a fili, sai dai cewa su a ƙarshe suna ƙunsar alheri mai girma, da hikima ta Ubanigiji mai isuwa.

31- Shin Addini ya haifar da yaƙoƙin Addini waɗanda suka mamaye ƙasa a cikin wani lokaci daga lokuta?

Amsa: Dan Adam ya rayu tare da shari'o;in tauhidi shekaru dubunnai, kuma tare da shari'o'in Ibrahim manya guda uku shekara dubu huɗu, Addini bai misalta wani haɗari ba kai tsaye, akan jinsin mutum, kai ya gabatar da darajoji na ɗabi'u maɗaukaka, waɗanda mumini da mulhidi suke haɗuwa akan su,,kuma ya kafa cigaba na asali, kai zai yiwu mu raya cewa, dukkanin wani alheri a ƙasa, to shi yana daga guraben waɗan can Annabcin ne! Haƙiƙa Addini ya hutar da kotuna daga dubban mas'aloli, sama da dukkanin wannan da wancan, Addini ya sanya tushe na sani da na hali da na darajoji, dan manufar samuwar mutum akan ƙasa! Kasashen da suka rungumi shari'o'in tauhidi, basu gushe ba zuwa yau suna mallakar nau'o'i na ilimi, wanda ya wanzarwa masu saɓani dasu, kuma ya basu rufin kariya da wabcin shari'o'in tauhidi su akan su, a yayin da cewa wani ƙarni guda ɗaya sashin ƙasashe sun kusanta a cikin sa ga ilhadin da mutuntaka ta kasance gaba ɗayan ta a gefen halaka! Sannan a yanzu mulhidai suzo suna zantar damu game da haɗarin Addini akan mutum! tarihin mutum bai san wani tsariba mafi haɗari fiye da ilhadi, mayankar Glag a tarayyar Soviet data gabata akan hannun mulhidi Vladimir Lenin, da halakar da mafiya ƙanƙantar dangantaka da bautar gumaka a Jamus ta Nazi, da ƙarar da ɗaya bisa huɗun mazauna Combodia, daga mutane a hannun mulhidi Pol Pot, da kashe 'yan China Miliyan 52 a cikin zanga-zangar babbar cigaban ilimi a hannun mulhidi

Mao Zedong, da bayyanar ƙungiyar mulhidai ta sojoji a turai wacce aka kulle a hukumance cibiya ta Addini dubu 42 - cocina da masallatai-aka kuma kashe gomman dubunnai daga masu Addini, sai ayyukan ilhadi da sakamakon ɗabi'a ga bayyanar ilhadi[32] kai lallai yaƙin duniya biyu na farko da na biyu, sun kasance yaƙoƙi ne na ilhadi, surantawa ta ilhadi ce take hukunta ta ga jinsinan mutum, da tinanikan tafiya wajen tsarkaka na asali, sai sakamakon ya kasance halakar da abin ya kusa kaiwa kaso biyar cikin ɗari na mazaunan duniya, kuma yaƙoƙin duniya suka maida kowane daga waɗanda sukayi nasara da waɗanda basuyi nasara ba ɗaya bisa uku na ƙarni zuwa koma baya, masana falsafa suka tashi da sanya mafitsara a cikin tsakiyar Paris wannan kinaya ne akan ƙarewar ci gaba, Kuma yaƙuna na ilhadi suka bar ma'ajiyar makaman No clear waɗanda suna isa dan halakar da jinsin mutum gaba ɗayan sa, sau da yawa Lallai cewa karatu kaɗan ga yaƙoƙin ƙarni na ashirin suna bayyanar da munin ilhadi. Haƙiƙa ilhadi ya bar a bayansa wani tinanin cewa gushewar jinsin mutum a kowane yaƙi mai gabatowa itace tinani tsayayye, wannan shine ayyukan ilhadi abin zatan afkuwar sa.

32- Me yasa musulmi suka ci baya duk da Addinin su na tauhidi, yayin da Yammaci suka ci gaba sosai?

Amsa: Wannan itace tambayar ci gaban zamani!

Da yawa Annabawa sun sha fama da fuskantar wannan tambayar.

Da yawa mabiya suka zame saboda dalilin wannan al'amarin.

tambayar ci gaba itace asalin kafircin al'ummatai tun a zamaninnika.

Allah - maɗaukakin sarki - Ya ce :

32 https://en.wikipedia.org/League-of-Militant-Atheisits -

﴿وَإِذَا تُتْلَىٰ عَلَيْهِمْ ءَايَٰتُنَا بَيِّنَٰتٍ قَالَ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ لِلَّذِينَ ءَامَنُوٓا۟ أَىُّ ٱلْفَرِيقَيْنِ خَيْرٌ مَّقَامًا وَأَحْسَنُ نَدِيًّا ﴿٧٣﴾﴾ [مريم: 73]

{Kuma idan anã karatun ãyõyinMu, bayyanannu a kansu, sai waɗanda suka kãfirta su ce wa waɗanda suka yi ĩmãni, "Wanne daga ƙungiyõyin biyu ya fi zama mafi alhẽri ga matsayi, kuma mafi kyaun majalisa?} {73} [Surat Maryam: 73].

Idan aka karanto ayoyin da a cikin su akwai hujjoji da dalilai akan ingancin Addini, kafairai sun kafa hujja da ci gaban al'ummatai kafirai. {Waɗan ne daga ƙungiyoyin biyu ya zama mafi alheri ga matsayi, kuma mafi kyawun majalisa}.

Mai bincike Ibrahim Al-Sakran - Allah Ya kiyaye shi - yana cewa; "Wannan ƙa'idace ta tarihi da sunna ta kasantuwa mai maimaituwa, mamaki baya ƙarewa daga lura da saƙonta mai suka a cikin rayuwa, to mafi yawan masu isarwa daga Allah tun lokacin ɓullar Annabc,i kuma har lokacin aikin Musulunci na zamani suna fuskanta a tsawon lokaci "Karfi na madda" tana wucesu kuma tana fitinar mutane daga bin wahayin da ke tare da su.

Kayi duba a cikin jarrabe-jarraben Annabawa, zaka samesu sun kusa su zama gaba ɗaya mutunmutumi mai magana dan ka yi tsakanin "Wahayin Ubangiji" da fitinar "Karfi na madda", kuma zaka samu fitinuwar mutane da ƙarfin maddar da take yaudarar hankulan su, kuma yana juyar dasu daga ƙanƙar da kai da miƙa wuya ga wahayi, kuma zaka samu masu aiki ga Addini suna fama da al'amuran biyu daga fitinar mutane da abubuwan bayyan na madda. Manzo na farko Nuhu - aminci ya tabbata a gare shi - mutanen sa su kace dashi da dukkanin madda ɓaro-ɓaro:

﴿فَقَالَ ٱلۡمَلَأُ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ مِن قَوۡمِهِۦ مَا نَرَىٰكَ إِلَّا بَشَرٗا مِّثۡلَنَا وَمَا نَرَىٰكَ ٱتَّبَعَكَ إِلَّا ٱلَّذِينَ هُمۡ أَرَاذِلُنَا بَادِيَ ٱلرَّأۡيِ وَمَا نَرَىٰ لَكُمۡ عَلَيۡنَا مِن فَضۡلِۭ بَلۡ نَظُنُّكُمۡ كَٰذِبِينَ ٢٧﴾ [هود: 27]

[Ba mu ganin wani ya bika face wadanda suke su ƙasƙantattunmu ne} {27}. [Surat Hud : 27].

Annabin Allah Musa bai bayyana ba har saida jerin shisshigin ƙarfi na birni yana maimaituwa daga sabo da ruɗinta a gaban wahayi.

﴿وَقَالَ مُوسَىٰ رَبَّنَآ إِنَّكَ ءَاتَيۡتَ فِرۡعَوۡنَ وَمَلَأَهُۥ زِينَةٗ وَأَمۡوَٰلٗا فِي ٱلۡحَيَوٰةِ ٱلدُّنۡيَا رَبَّنَا لِيُضِلُّواْ عَن سَبِيلِكَۖ رَبَّنَا ٱطۡمِسۡ عَلَىٰٓ أَمۡوَٰلِهِمۡ وَٱشۡدُدۡ عَلَىٰ قُلُوبِهِمۡ فَلَا يُؤۡمِنُواْ حَتَّىٰ يَرَوُاْ ٱلۡعَذَابَ ٱلۡأَلِيمَ ٨٨﴾ [يونس: 88]

{Musa yace ya Ubangijinmu lallai cewa kaine kabaiwa Fir'auna da majalisar sa ƙawa da dukiyoyi a cikin rayuwar duniya, ya Ubangijin mu domin su ɓatar (da mtane) daga hanyarka] {88}. [Surat Yunus : 88].

Halin bai kasance sabo ba, dangane da Annabin mu Muhammad - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi - haƙiƙa ya kasance masu musun Annabcin sa da wahayin da ke tare da shi, suna dogaro a wajen bijirewa daga gare shi da raunin sa na madda.

﴿وَقَالُواْ لَوۡلَا نُزِّلَ هَٰذَا ٱلۡقُرۡءَانُ عَلَىٰ رَجُلٖ مِّنَ ٱلۡقَرۡيَتَيۡنِ عَظِيمٍ ٣١﴾ [الزخرف: 31]

{Kuma suka ce: "Don me ba a saukar da wannan Alƙur'ãni a kan wani mutum mai girma daga alƙaryun nan biyu ba?} {31}. [Surat Al-Zukhruf : 31].

Zancen Ibrahim Al-sakran ya ƙare.

Ba'a jarrabi mutum a tsawon zamaninnika ba da kuma tsawon tarihin Annabta da wani bala'i mafi girma fiye da fitinuwa da ƙarfin madda ga kafiri.

Tare da cewa babu wata alaƙa tun asali tsakanin cigaba da gaskiya.

Ci gaba na madda, da ci baya babu wata alaƙa garesu da wanda gaskiya ko ƙarya ke tare dashi.

Baya lazimta daga kasancewar mutum mafifici kuma managarci, da ya kasance mai ci gaba kuma mai wayewa ta zamani.

Mutum zai iya kasancewa, mai lazimtuwa da koyarwar Musulunci, sai dai cewa shi talakane sosai, kuma akasin haka zai iya kasancewa.

Da yawa daga al'ummatai sun kasance masu cigaban zamani, alhali su suna daga mafi nisantar mutane daga shari'ar Allah da Addinin Sa da wahayin Sa.

﴿أَوَلَمۡ يَسِيرُواْ فِي ٱلۡأَرۡضِ فَيَنظُرُواْ كَيۡفَ كَانَ عَٰقِبَةُ ٱلَّذِينَ مِن قَبۡلِهِمۡۚ كَانُوٓاْ أَشَدَّ مِنۡهُمۡ قُوَّةٗ وَأَثَارُواْ ٱلۡأَرۡضَ وَعَمَرُوهَآ أَكۡثَرَ مِمَّا عَمَرُوهَا وَجَآءَتۡهُمۡ رُسُلُهُم بِٱلۡبَيِّنَٰتِۖ فَمَا كَانَ ٱللَّهُ لِيَظۡلِمَهُمۡ وَلَٰكِن كَانُوٓاْ أَنفُسَهُمۡ يَظۡلِمُونَ ٩﴾ [الروم: 9]

{Shin baza suyi tafiya acikin ƙasa bane sai suyi duba yaya ƙarshen waɗanda ke gaban su ya kasance sun kasance mafi tsananin ƙarfi daga garesu da kuma suka nomi ƙasa, suka rayata fiye da yadda suka rayata} {9}. [Surat Al-Rum : 9].

Cigaba na madda da dukiya, basu zamo ma'auni akan ma'abocin gaskiya ba.

﴿فَلَمَّا جَآءَتۡهُمۡ رُسُلُهُم بِٱلۡبَيِّنَٰتِ فَرِحُواْ بِمَا عِندَهُم مِّنَ ٱلۡعِلۡمِ وَحَاقَ بِهِم مَّا كَانُواْ بِهِۦ يَسۡتَهۡزِءُونَ ٨٣﴾ [غافر: 83]

{A lõkacin da Manzanninsu suka jẽ musu da hujjõji bayyanannu, suka yi farin ciki da abin da ke wurinsu na ilmi kuma abin da suka kasance sunã yi na izgili da shi ya wajaba a kansu} {83}. [Surat Al-gafir : 83].

A wannan lokacin cigaba na madda bai zamo abin yaboba akan kansa, haka nan shi ba abin zargi bane a kan kansa, kaɗai ana yaban sa ne gwargwadan tsarkakeshi da wahayin Ubangiji, kuma da gwaargwadan ɗabbaka Addini acikin sa, da gwargwadan amfanuwar ka da shi a cikin Addinin ka, kuma da gwargwadan a binda kake amfani da shi a cikin amfanar mutane da gyara halayen su saboda Allah.

Wannan shine cigaba abin nema.

Ma'aunin fifiko na haƙiƙa tsakanin mutane, bai zamo a cikin cigaban su na madda ba sai dai a cikin fifiko ne da tsoron Allah da aiki na gari, kuma cigaba na madda yana zuwa ne kamar wani tsani, amma ba wai manufa ba...zaizo kamar tsani dan yin hidima da amfanar mutane saboda Allah.

Sai ya zama cigaba na madda abin tsarkakewa da whayin Ubangiji, kuma shi, shi kaɗaine cigaba abin nema.

Wannan shine mayewa ta haƙiƙa a kan ƙasa: Mayewa ta bauta ga Allah, da mayewa ta tsarkakewa ta imani ga kowane ɓangarorin rayuwa.

﴿ٱلَّذِينَ إِن مَّكَّنَّٰهُمۡ فِي ٱلۡأَرۡضِ أَقَامُواْ ٱلصَّلَوٰةَ وَءَاتَوُاْ ٱلزَّكَوٰةَ وَأَمَرُواْ بِٱلۡمَعۡرُوفِ وَنَهَوۡاْ عَنِ ٱلۡمُنكَرِۗ وَلِلَّهِ عَٰقِبَةُ ٱلۡأُمُورِ ٤١﴾ [الحج: 41]

{Waɗanda suke idan Muka bã su ĩko a cikin ƙasa sai su tsai da salla, kuma su bayar da zakka kuma su yi umurni da abin da aka sani, kuma su hana daga abin da ba a sani ba. Kuma ãƙibar al'amura ga Allah take} {41}. [Surat Al-Hajj: 41].

Ka sani cewa musulmi idan ya aikata abinda ke kansa, to Allah zai sawwaƙa masa dalilan dukkan alheri da arziƙi da cigaba a duniya, da tsira da ɗaukakar daraja a lahira.

﴿وَعَدَ ٱللَّهُ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ مِنكُمۡ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ لَيَسۡتَخۡلِفَنَّهُمۡ فِي ٱلۡأَرۡضِ كَمَا ٱسۡتَخۡلَفَ ٱلَّذِينَ مِن قَبۡلِهِمۡ وَلَيُمَكِّنَنَّ لَهُمۡ دِينَهُمُ ٱلَّذِي ٱرۡتَضَىٰ لَهُمۡ وَلَيُبَدِّلَنَّهُم مِّنۢ بَعۡدِ خَوۡفِهِمۡ أَمۡنٗاۚ يَعۡبُدُونَنِي لَا يُشۡرِكُونَ بِي شَيۡـٔٗاۚ وَمَن كَفَرَ بَعۡدَ ذَٰلِكَ فَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡفَٰسِقُونَ ٥٥﴾ [النور: 55]

{Allah Ya yi wa'adi ga waɗanda suka yi ĩmãni daga gare. Ku, kuma suka aikata ayyukan ƙwarai, lalle zai shugabantar da su a cikin ƙasa kamar yadda Ya shugabantar da waɗanda suke daga gabãninsu, kuma lalle ne zai tabbatar musu da addininsu wanda Ya yardar musu, kuma lalle ne Yanã musanya musu daga bãyan tsõronsu da aminci, sunã bauta Mini bã su haɗa kõme da Nĩ. Kuma wanda ya kãfirta a bãyan wannan, to, waɗancan, su ne fãsiƙai} {55}. [Surat Al-Nur: 55}.

Lokacin da musulmi suka ɗabbaka Addininsu, sun kasance shugabanni a cikin Addini da duniya.

Musulunci ya gabatar da wani cigaba na wayewa a hannayen su, wanda ya zarce shekara 1200, kuma itace mafi tsawon wayewa da ta zarce, ba tare da tsayawa ba ko yankewar wannan muddar.

Wayewa ta Musulunci ta taso tare da musulunci.

Shi da wannan Addinin kaɗaitacce, wanda ya farar da wani cigaba na zamani.

Ragowar Addinai wasu cigaban su suka renesu.

Zamu samu cigaba na yamma kiristanci ya rene shi, cigaba na hindu kuma Addinin Hundus ya rene shi.

Amma Addini ɗaya wanda ya farar da cigaban zamani to shine: Musulunci.

Yayin da musulmai suka kasance, suna sanin abinda ya lazimce su daura da Addinin su, suka jagoranci duniya a madda da rai.

Lokacin da Musulunci ya shiga Kusdndiniyya shekara ta 1453 M, sai zamaninnikan na tsakiya masu duhu suka ƙare a Turai.

Tarihin ƙarewar zamaninnika masu duhu, shine 1453 M, shine ainihin shekarar da Musulunci ya shiga turai a cikinta.

Musulunci bai zamo ya shiga zuciyar Turaiba har sai da hasken ilimi ya haskaka a cikita.

A cikin library na Congress (Taro na masu ruwa da tsaki) an rubuta akan rufin babbakin ɗakin taro na library wasu kewaye da suke nuni zuwa asalin gabatuwar cigaban zamanin mutanen yamma, Musulunci shine Addini ɗaya abin ambata a cikin kewan guda bakwai.

Musulunci shine Addini guda ɗaya abin ambata, shine yake keɓantuwa da ilimummuka na ɗabi'a.

ISLAM; PHYSICS

Yayin da ragowar kewayen yake keɓantar sunayen wasu garuruwa da abin da waɗan nan garuruwan suka gabatar shine cigaba na Adabi ko na ƙirƙira ko na yare.

Musulunci ya gabatar da ilimi, a tsawon shekara 700 yaran ƙasashe na ilimummuka a duniya ya kasance shine: yaran larabci.[33]

Idan musulmai suka gyara Addinin su, to duniyar su zata gyaru.

33- Menene fa'idar bautar Allah - tsarki ya tabbatar maSa Ya ɗaukaka -

33 https"//www.telegraph.co.uk/news/science/science-news/3323462/Science-Islams-forgotten-geniuses.html

Amsa: Mutum da ɗabi'ar sa wacce aka halicceshi akanta, bai san zatin sa ba, kuma ransa baya nutsuwa, kuma kewar zuciyar sa bata nutsuwa sai da bautar Allah

﴿ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَتَطۡمَئِنُّ قُلُوبُهُم بِذِكۡرِ ٱللَّهِۗ أَلَا بِذِكۡرِ ٱللَّهِ تَطۡمَئِنُّ ٱلۡقُلُوبُ ٢٨﴾ [الرعد: 28]

{Waɗanda suka yi ĩmãni kuma zukãtansu sukan natsu da ambaton Allah. To, da ambaton Allah zukãta suke natsuwa} {28}. [Surat Al-Ra'ad: 28].

Da ibada ne ƙirji yake nutsuwa.

﴿وَلَقَدۡ نَعۡلَمُ أَنَّكَ يَضِيقُ صَدۡرُكَ بِمَا يَقُولُونَ ٩٧ فَسَبِّحۡ بِحَمۡدِ رَبِّكَ وَكُن مِّنَ ٱلسَّٰجِدِينَ ٩٨﴾ [الحجر: 97-98]

{Kuma lalle ne haƙĩƙa Munã sanin cẽwa lalle kai, ƙirjinka yanã yin ƙunci game da abin da suke faɗã (na izgili)} [97]. {Ka tsarkake da godiyar Ubangijinka kuma ka kasance daga masu sujjada} {98}. {Kuma ka bautawa Ubangijin ka}. [Surat Al-Hijr: 97-98].

Ka bautawa Ubangijin ka: Sai ƙirjinka ya nutsu.

Saboda haka ne raka'a biyu da khushu'i da bibiyar ma'anonin karatun sallar suna yin abinda lokutan zaman sawa rai nutsuwa ba sayi a cikin ran mutum.

Ibada acikinta akwai nutsuwar ran mutum, kuma dukkan wanda ya nisanta daga ambatan Allah ƙirjinsa zaiyi ƙunci, sai ka same shi koda yaushe yana baƙin ciki akan duniya, shi baya ƙoshi kuma baya nutsuwa.

﴿وَمَنۡ أَعۡرَضَ عَن ذِكۡرِي فَإِنَّ لَهُۥ مَعِيشَةٗ ضَنكٗا وَنَحۡشُرُهُۥ يَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِ أَعۡمَىٰ ١٢٤﴾ [طه: 124]

{Duk wanda ya bijire daga ambatona (Al-ƙur'ani) to ƙuntatacciyar rayuwa ta tabbata gare shi} {124}. [Surat Daha : 124].

Duk yadda mutum ya kasance a cikin yalwa ta arziƙi sai dai cewa shi baya tare da imani, yana rayuwa a cikin ƙunci, kuma a cikin tsere abin sawa zazzaɓi wanda bazai ƙare tare da abin jahilta ba, sai ka ganshi koda yaushe mara nutsuwar rai.

Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi - ya ce : "Duk wanda duniya ta zama manufar sa Allah zai tarwatsa masa al'amarin sa, kuma ya sanya talaucin sa tsakanin idanuwan sa, babu abinda zaizo masa na duniya sai abin da aka rubuta masa, duk wanda lahira ta zama niyyar sa Allah Zai taro masa al'amarin sa, kuma zai sanya wadatar sa a cikin zuciyar sa, kuma duniya zatazo masa alhali ita tana ƙasƙantacciya"[34] .

Ibada tana 'yanto musulmi daga ƙasƙantar da kai ga duniya, kuma tana maida shi ɗa (ba bawa ba).

Saboda haka musulmin da yake bautawa Allah da gaskiya, shine mutumin da ya fahimci ma'anar rayuwa, kuma ya fahimci ƙimar duniya, ya fahimci manufar samuwar sa a cikin wannan duniyar, kuma ya fahimci cewa shi a cikin wannan duniyar za'a jarraba shi, kuma zai bautawa Ubangijin sa haƙiƙanin bauta, bai zamo dan ya rayu a cikin

34 Sahihu Sunan Al-Tirmizi, H:2465.

rashin nutsuwar rai ba, ba tare da wata fa'ida a ƙarƙashin sa ba, Ubangijin mu - tsarki ya tabbatar maSa - Ya ce :

﴿ٱلَّذِي خَلَقَ ٱلۡمَوۡتَ وَٱلۡحَيَوٰةَ لِيَبۡلُوَكُمۡ أَيُّكُمۡ أَحۡسَنُ عَمَلٗاۚ وَهُوَ ٱلۡعَزِيزُ ٱلۡغَفُورُ ۝٢﴾ [الملك: 2]

{Shi ne Wanda Ya halitta mutuwa da rãyuwa domin Ya jarraba ku, Ya nũna wãye daga cikinku ya fi kyãwon aiki} {2}. [Surat AlMulk : 2].

34- Waɗanne ne mabayyanan (alamomin) miƙa wuya ga Allah - maɗaukakin sarki - ? ko da wata sigar daban : Ta yaya za kasan cewa kai mai miƙa wuya ne ga Allah, miƙa wuya cikakke ?

Amsa : Alamomin miƙa wuya ga Allah - maɗaukakin sarki - guda huɗu ne sune :

Na daya : Tabbatar da bauta ga Allah a cikin kowane abu ƙarami da babba, acikin rayuwar ka, Allah - maɗaukakin sarki - Ya ce :

﴿قُلۡ إِنَّ صَلَاتِي وَنُسُكِي وَمَحۡيَايَ وَمَمَاتِي لِلَّهِ رَبِّ ٱلۡعَٰلَمِينَ ۝١٦٢ لَا شَرِيكَ لَهُۥۖ وَبِذَٰلِكَ أُمِرۡتُ وَأَنَا۠ أَوَّلُ ٱلۡمُسۡلِمِينَ ۝١٦٣﴾ [الأنعام: 162-163]

{Ka ce: "Lalle ne sallãta, da baikõna, da rãyuwãta, da mutuwãta, na Allah ne Ubangijin tãlikai} {162}. {Bãbu abõkin tãrayya a gare Shi. Kuma da wancan aka umurce ni, kuma ni ne farkon mãsu sallamãwa} {163}. [Surat Al-An'am: 162-163].

Salla ta, da yanka na, da rayuwa ta, da mutuwa ta, na Allah ne Ubangijin talikai: Kowane abu da nake aikata shi, to na Allah ne, ni ina yin sallah saboda Allah, ina bin mahaifa na saboda Allah, ina muzakara ina neman ilimi har in anfanar da mutane saboda Allah ne, ina yin bacci don in zama mafi ƙarfi a gobe, akan aikin abin da Allah Ya umarceni da shi.

Ita bauta ce ga Allah a kowane aiki, wannan suna daga mafi muhimmancin mabayyana, da alamomi miƙa wuya ga Allah.

Alama ta biyu har ka zama mai miƙa wuya ga Allah, cikakken miƙa wuya: Itace bin abin da Allah Yayi umarni da shi, da nisantar abin da Yayi hani gare shi, Ubangijin mu - tsarki ya tabbatar maSa - Ya ce:

﴿يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ ٱدۡخُلُواْ فِي ٱلسِّلۡمِ كَآفَّةٗ وَلَا تَتَّبِعُواْ خُطُوَٰتِ ٱلشَّيۡطَٰنِۚ إِنَّهُۥ لَكُمۡ عَدُوّٞ مُّبِينٞ ٢٠٨﴾ [البقرة: 208]

{Yã ku waɗanda suka yi ĩmãni! Ku yi ɗã'a ga Allah da ManzonSa, kuma kada ku jũya daga barinSa, alhãli kunã ji} {20}. [Surat Al-Anfal: 20]. Allah - maigirma da ɗaukaka - Ya ce: {Yaku waɗanda sukayi imani ku shiga cikin Musulunci gaba ɗaya} {208}. [Surat Al-Baƙara: 208].

Fis Silmi wato: A cikin Musulunci.

Ku shiga cikin Musulunci gaba ɗaya: Wato ku lazimci dukkanin a bin da Allah yayi umarni da shi, ku kuma hanu daga abin da Yayi hani daga gare shi.

Allah Ya umarce ni da wani abu da zan aikatashi,... ya haneni daga wani abu zan hanu daga gare shi, to wannan shine cikakken miƙa wuya da jawuwa ga Allah.

Alama ta uku akan miƙa wuya ga Allah itace: Mu miƙa wuya da aiwatar da abin da Allah Ya shara'anta, sai mu yarda da shari'ar Sa mu karɓe ta.

Mu karɓi dukkanin shari'ar Allah, misali kada muyi musun uƙubobin da Allah Ya shara'anta su, kai babu makawa mu yarda da shari'ar Allah, domin Allah Yana sanin abin da Yake gyara halittatar Sa, kuma Yana sanin cewa, akwai tsarkaka ga al'umma a cikin waɗan nan uƙubobin

﴿أَلَا يَعْلَمُ مَنْ خَلَقَ وَهُوَ ٱللَّطِيفُ ٱلْخَبِيرُ ۝١٤﴾ [الملك: 14]

{Ashe wanda yayi halitta ba zai iya saninta ba, alhali kuwa shi Mai tausayine Mai labartawa} {14}. Surat Al-Mulk.

Kuma tsarki ya tabbatar maSa Ya ce:

﴿أَفَحُكْمَ ٱلْجَٰهِلِيَّةِ يَبْغُونَ ۚ وَمَنْ أَحْسَنُ مِنَ ٱللَّهِ حُكْمًا لِّقَوْمٍ يُوقِنُونَ ۝٥٠﴾ [المائدة: 50]

{Wanene mafi kyau ga hukunci daga Allah} {50}. [Surat Al-Ma'idah: 50].

Allah shine Yake sanin abin da Yake gyara mutane a cikin duniyar su da lahirar su.

Dabbaƙa shari'ar Allah, yana tsarkake mutane kuma yana sanya su suna rayuwa a cikin aminci.

Wani mutum ya tafi yana riya cewa, shi yayi imani da Allah da kuma abin da aka saukar ga Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi - zuwa Ka'abu ɗan Al-Ashraf Bayahude dan yayi masa hukunci a cikin wata mas'ala daga mas'aloli, maimakon ya tafi gurin Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata agareshi - dan tsoron Manzo - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi - yayi hukunci da wani hukuncin da

ba zai ƙayatar dashi ba, sai ya tafi wurin Bayahude dan buri a cikin hukuncin da zai ƙayatar da shi, sai faɗin Allah maɗaukakin sarki - ya sauka -:

﴿أَلَمۡ تَرَ إِلَى ٱلَّذِينَ يَزۡعُمُونَ أَنَّهُمۡ ءَامَنُواْ بِمَآ أُنزِلَ إِلَيۡكَ وَمَآ أُنزِلَ مِن قَبۡلِكَ يُرِيدُونَ أَن يَتَحَاكَمُوٓاْ إِلَى ٱلطَّٰغُوتِ وَقَدۡ أُمِرُوٓاْ أَن يَكۡفُرُواْ بِهِۦۖ وَيُرِيدُ ٱلشَّيۡطَٰنُ أَن يُضِلَّهُمۡ ضَلَٰلَۢا بَعِيدٗا ٦٠﴾ [النساء: 60]

{Shin, ba ka gani ba, zuwa ga waɗanda suke riyãwar cẽwa sunã ĩmãni da abin da aka saukar zuwa gare ka da abin da aka saukar daga gabãninka, sunã nufin su kai ƙãra zuwa ga ¦ãgũtu alhãli kuwa, lalle ne, an umurce su da su kãfirta da shi, kuma Shaiɗan yanã nẽman ya ɓatar da su, ɓatarwa mai nĩsa} {60}. [Surat Al-Nisai: 60]

Idan ka zama musulmi mai jawuwa ga Allah, to ya wajaba akan ka ka lazimtu da shari'ar Allah, kuma ka miƙa wuya ga hukuncin Allah, ko da hukuncin Allah yazo ba akan san ranka ba, ba kabar shari'ar Allah ba, kuma ka tafi ga wani Bayahude dan yayi maka hukunci a cikin mas'alar ka, dan ya yardar da kai.

Allah - mai girma da ɗaukaka - Ya faɗa a cikin ayoyin nan masu zuwa:

﴿وَمَآ أَرۡسَلۡنَا مِن رَّسُولٍ إِلَّا لِيُطَاعَ بِإِذۡنِ ٱللَّهِۚ وَلَوۡ أَنَّهُمۡ إِذ ظَّلَمُوٓاْ أَنفُسَهُمۡ جَآءُوكَ فَٱسۡتَغۡفَرُواْ ٱللَّهَ وَٱسۡتَغۡفَرَ لَهُمُ ٱلرَّسُولُ لَوَجَدُواْ ٱللَّهَ تَوَّابٗا رَّحِيمٗا ٦٤﴾ [النساء: 64]

{Ba mu aiko wani Manzo ba sai dan ayi masa ɗa'a da izinin Allah} {64} Surat Al-Nisa'i.

Allah bai aiko Manzanni ba dan mu barta mu nemi hukuunci zuwa ga wata shari'ar da ba ita ba.

Sannan Allah - mai girma da ɗaukaka - Ya rufe darasin, daga wannan abin da ya faru, da masu kama da ita, da wata aya mai muhimmanci da take bayyana larurar ƙanƙar da kai dan neman hukunci ga shari'ar Allah, Ubangijin mu - mai girma da ɗaukaka - Ya ce:

﴿فَلَا وَرَبِّكَ لَا يُؤْمِنُونَ حَتَّىٰ يُحَكِّمُوكَ فِيمَا شَجَرَ بَيْنَهُمْ ثُمَّ لَا يَجِدُواْ فِيٓ أَنفُسِهِمْ حَرَجًا مِّمَّا قَضَيْتَ وَيُسَلِّمُواْ تَسْلِيمًا ۝٦٥﴾ [النساء: 65]

{To, a'aha! Ina rantsuwa da Ubangijinka, ba za su yi ĩmãni ba, sai sun yarda da hukuncinka ga abin da ya sãɓa a tsakãninsu, sa'an nan kuma ba su sãmi wani ƙunci a cikin zukãtansu ba, daga abin da ka hukunta, kuma su sallama sallamãwa} {65}. Suta Al-Nisai,

i: Babu makawa daga miƙa wuya cikakke ga bain da Allah Ya shara'anta, miƙa wuya ga shari'ar Allah, yana daga alamomin jawuwa ga Musulunci!

Amma alama ta huɗu, akan miƙa wuya ga Allah - maɗaukakin sarki - itace: Miƙa wuya ga ƙaddarorin Allah, duk abin da Allah - tsraki ya tabbatar maSa - ya ƙaddara shi da hikimar Sa, bayan nan musulmi yana miƙa wuya ga Allah a cikin dukkanin ƙaddarorin Sa... a cikin alheri da sharri.

Idan farin ciki ya sami musulmi sai ya gode, idan cuta ta same shi sai yayi haƙuri.

Da ace Allah zai azirta ka da wani abinci, ko wani arziƙi mai kyau, ko wani gida mai kyau, ko nasara acikin karatu, ko lafiya a cikin jiki, ko iyalai na gari zaka godewa Allah.

Da ace cuta zata samu musulmi ta rashin lafiya ce ko talauci ko tsoro ko bala'i ko baƙin ciki, yayi haƙuri a bisa waɗan nan cutukan ya nemi taimako da Allah, to wannan shine halin musulmi mai jawuwa mai miƙa wuya ga Ubangijin sa - tsarki ya tabbatar maSa -.

Kowane abu yana kasancewa da ƙaddarawar Allah - mai girma da ɗaukaka -: lafiya da rashin lafiya da talauci... kowane abu da ƙaddarawar Sa ne, da kuma hikimar Sa, ya wajaba akan musulmi yarda da ƙaddarori, domin cewa Allah Shine wanda Yake ƙaddara su.

Ubangijin mu tsarki ya tabbatar maSa Yace:

﴿إِنَّا كُلَّ شَيۡءٍ خَلَقۡنَٰهُ بِقَدَرٖ ٤٩﴾ [القمر: 49]

{Lalle Mũ, kõwane irin abu Mun halitta shi a kan tsãri} {49}. [Surat Al-Kamar : 49].

kuma Allah - maɗaukakin sarki - Ya ce:

﴿قُل لَّن يُصِيبَنَآ إِلَّا مَا كَتَبَ ٱللَّهُ لَنَا هُوَ مَوۡلَىٰنَاۚ وَعَلَى ٱللَّهِ فَلۡيَتَوَكَّلِ ٱلۡمُؤۡمِنُونَ ٥١﴾ [التوبة: 51]

{Kace babu abin da zai same mu sai abin da Allah Ya rubuta mana} {51}. [Surat Al-Taubah: 51].

Babu abinda zai same mu sai abin da Allah ya ƙaddara mana.

(Allah) - mai girma da ɗaukaka - Ya ce:

﴿وَمَا كَانَ لِنَفْسٍ أَن تَمُوتَ إِلَّا بِإِذْنِ ٱللَّهِ كِتَٰبًا مُّؤَجَّلًاۗ وَمَن يُرِدْ ثَوَابَ ٱلدُّنْيَا نُؤْتِهِۦ مِنْهَا
وَمَن يُرِدْ ثَوَابَ ٱلْأَخِرَةِ نُؤْتِهِۦ مِنْهَاۚ وَسَنَجْزِى ٱلشَّٰكِرِينَ ١٤٥﴾ [آل عمران: 145]

{Babu wani rai da ta kasance zata mutu saida izinin Allah} {145}. [Surat Aal-Imran : 145].

Ajalillika Allah Ya ƙaddara su.

Dukkanin abin da yake faruwa a cikin kasantacce, kuma dukkanin wata ƙwayar komayyar da take tafiya a duniya, kuma dukkanin wani fararren da yake faruwa, kaɗai yana faruwa ne da sanin Allah da mashi'ar Allah, da kuma ƙaddarawar Allah, da kuma hikimar Allah, da kuma ikon Allah.

Ubangijin mu tsarki ya tabbatar maSa Ya ce :

﴿ٱلَّذِى لَهُۥ مُلْكُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ وَلَمْ يَتَّخِذْ وَلَدًا وَلَمْ يَكُن لَّهُۥ شَرِيكٌ فِى ٱلْمُلْكِ
وَخَلَقَ كُلَّ شَىْءٍ فَقَدَّرَهُۥ تَقْدِيرًا ٢﴾ [الفرقان: 2]

{Kuma Ya halicci kowane abu, saboda haka Ya ƙaddara shi ƙadartawa} {2}. [Surat Al-Furƙan : 2].

Shi - tsarki ya tabbatar maSa - Ya halicci komai kuma Ya ƙaddara komai, abin da Yaso zai kasance, abinda Bai so ba bazai kasance ba.

Ni a matsayi na na musulmi, abin nema ne da miƙa wuya ga dukkanin ƙaddarorin Allah - mai girma da ɗaukaka -.

Da wannan ne mutum yake wayar gari mai miƙa wuya ga Allah.

## A ƙarshe! Ta yaya zan shiga Musulunci?

Musulunci shine Addinin Allah ga dukkanin mutane, Allah - maɗaukakin sarki - Ya ce:

﴿إِنَّ ٱلدِّينَ عِندَ ٱللَّهِ ٱلۡإِسۡلَٰمُۗ وَمَا ٱخۡتَلَفَ ٱلَّذِينَ أُوتُواْ ٱلۡكِتَٰبَ إِلَّا مِنۢ بَعۡدِ مَا جَآءَهُمُ ٱلۡعِلۡمُ بَغۡيَۢا بَيۡنَهُمۡۗ وَمَن يَكۡفُرۡ بِـَٔايَٰتِ ٱللَّهِ فَإِنَّ ٱللَّهَ سَرِيعُ ٱلۡحِسَابِ ١٩﴾ [آل عمران: 19]

{Lallai Addini a wurin Ubangiji (shine) Musulunci} {19} [Surat Aal-Imran: 19]

Musulunci shine Addinin da Allah baYa karɓar wanin sa daga Addinai.

﴿وَمَن يَبۡتَغِ غَيۡرَ ٱلۡإِسۡلَٰمِ دِينٗا فَلَن يُقۡبَلَ مِنۡهُ وَهُوَ فِي ٱلۡأٓخِرَةِ مِنَ ٱلۡخَٰسِرِينَ ٨٥﴾ [آل عمران: 85]

{Kuma wanda ya nẽmi wanin Musulunci ya zama addini, to, bã zã a karɓa daga gare shi ba. Kuma shi a Lãhira yana daga cikin mãsu hasãra} {85}. [Surat Aal-Imran: 85].

Saboda haka yana wajaba akan kowane mutum da ya rungumi Musulunci.

A Musuluncine ake samun tsira daga wuta da rabauta da yardar Allah da kuma Aljanna.

Shiga cikin Musulunci wata ni'imace daga mafi girman ni'imomi, kai shine ma mafi girma kuma mafi muhimmancin abu a cikin samuwar ka.

Musulunci a cikin haƙiƙar sa komawane zuwa ɗabi'ar da aka halicci mutum akan ta da kuma hankali.

Shiga cikin Musulunci, al'amarin sa mai sauƙi ne, baya buƙatuwa zuwa wasu tsare-tsare na ibadu, ko tarurruka, da wasu alamomi (kamar yanda Kiristoci sukeyi), ko wasu al'amura a hukumance, kawai wajibi akan mutum yayi furuci da shahadodi biyu: Wannan da ya ce: Ina shaidawa babu abin bautawa da gaskiya sai Allah, kuma ina shaidawa cewa (Annabi) Muhammadu Manzon Allah ne.

Shi da wannan ne ya zama musulmi.

Sannan ya fara ayyukan Musulunci.

Ina yin wasiyya da bibiyar shafin yanar gizo na islamhouse, kowa gwargwadan yarens a, har sabon musulmi yasan ta yaya zaiyi Musulunci.

URS na shafin yanar gizon : /https://islamhouse.com/ar

## Contents

Tambaya da amsa ........................................................ 4

A ƙarshe! Ta yaya zan shiga Musulunci?...................... 110

Contents ........................................................ 112